**COURSE GUIDE**

# HAU 207
# SURVEY OF HAUSA ORAL LITERATURE
# (BAYANI GAME DA ADABIN BAKA NA HAUSA)


**Course Team** Dr. Aliyu Isa Suleiman (Course Writer) - Kaduna State University, Kaduna
Professor Ibrahim Malumfashi (Course Editor) - Kaduna State University, Kaduna



**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

© 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Printed 2023

ISBN: 978-978-058-875-5

## CONTENTS

Gabatarwa (Introduction)
Manufar Wannan Kwas (Course Aim)
Koyo Tsantsa (Working Through the Course)
Kashe-kashen Darasi (Study Units)
Manazarta da Abubuwan Qara Nazari
Auna Fahimta (Assignment)
Jinga (Tutor Marked Assignment)
Jarrabawa (Final Examination and Grading)

**Gabatarwa (Introduction**)

Wannan darasi na Hau 207, kwas ne da ke bayani game da adabin baka na Hausa. Abubuwan dake cikin wannan manhaja suna gabatar da wannan darasi ne tun daga ma'ana ita kanta kalmar adabin baka da yadda ake iya gane adabin baka. Haka nan kuma an yi bayanin Yadda ake tattara adabin baka waxanda suka haxa da kula da rashin rubutu da shekaru da yadda al`ada take da kumyiwuwar ragi ko qari da za a iya samu yayin tattara adabin baka. Wannan manhaja tana bayani kan abin da kwas ya qunsa da kuma abubuwan da kwas yake bukata da kuma bayanan da xalibai za su yi amfani da su domin fahimtar kwas sosai da sosai.

Manhajar na bayanin irin abubuwan da suka kamata ga xalibi ya kiyaye a yayin da yake nazarta kowane kashi. Hakanan kuma, manhajar ta kawo tambayoyi waxanda ake bukatar mai nazari ya amsa, don yin haka zai taimaka wajen fahimtar abin da kwas din yake koyarwa. Yana da kyau idan an sami matsololi ko rashin fahimtar wani kashi ko darasi a garzaya faxin haka a yayin tattaunawa da malaman dake kula ko koyar da wannan darasin. Ya zama wajibi a rinqa tuntubar malami ko malamai kan wasu abubuwan da suka shigewa xalibai duhu a yayin da ake tattaunawa tsakanin malamai da xalibai (tutorial class). Yin haka zai taimaka ainun wurin samun nasarar isar da saqo ga xalibi.

**Manufar Wannan Kwas (Course Aim)**

An karkasa wannan kwas na HAU 207 zuwa kashi kashi, a kowane kashi, akwai muhimman abubuwa da ake fatar xalibai su sani game da kowane kashin da aka gabatar, wato manufar da ake qoqarin a cimmawa yayin da aka kammala karatun wannan kashin. Don haka, a karanta manufar da kyau a kuma fahimce ta sosai da sosai. Da zarar an san manufar da wannan kashi ko darasi take fatar ta cimma wa, to xalibai za su iya gwada qimar ganewarsu ko rashin gane darasin da suka karanta.

Wannan darasi na (HAU: 207) yana da muhimman manufofin da yake qoqarin isar waga mai karatu waxanda suka haxa da:

- Ma'ana da rabe raben adabin baka
- Yadda ake Gane adabin baka
- Yadda ake tattara adabin baka
- Wasu daga cikin zantukan baka na Hausa

**Koyo Tsantsa (Working Through the Course)**

Yana da kyau mai karatu ya nazarci kowane kashi a tsanake tare da bibbiyar manazartar da aka gabatar domin qarin haske da samun qarin bayanai. Sanannen abu ne cewa Hukumar NOUN ta tanadar wa xalibai muhimman abubuwa da xakin karatu duk ta yanar gizo waxanda za su

taimakawa xalibi karatu daga gida, ba don komai ba sai don inganta karatunsu da kaifafa fahimtar abin da aka sawa gaba. A qarshen kowane kasha na wannan kwas, akwai tambayoyi, su waxannan tambayoyin anyi su ne domin su auna fahimtar mai karatu dangane da abin daya karanta. Haka nan kuma akwai tambayoyin auna fahimta waxanda aka tsara domin xalibai. Ana bukatar idan an amsa waxannan tambayoyi, to a miqa amsoshin ga malaman da ke kula da darasin domin a duba a kuma bayar da sakamakon da ya cancanta. Su waxannan ayyuka na "Jinga" da aka ba xalibai suna taimakawa wajen harhaxa sakamakon jarabawar qarshen zangon karatu, domin fitar da sakamakon kowane kwas da xalibai suka yi. Rukunai guda huxu wannan kwas na HAU 207 yake da su, a kowane rukuni akwai kashi- kashi huxu-huxu, saboda haka ana sa ran xalibai su kammala wannan kwas cikin satuttuka goma sha shida kwatankwacin yawan kashin da ake da su. Kowane rukuni yana da alaqa da mai bi masa, haka nan kowane kashi yana da dangantaka da mai biye da shi. Saboda haka, kada xalibai su tsallake wani kashi zuwa wani kashi, yin haka kan gurgunta fahimta da rashin gane abin da kwas yake koyarwa.

Tsara lokacin karatu da xalibai za su yi daidai da yawan kashe-kashen da ke kowane kwas ita ce muhimmiyar shawarar da ake ba su, saboda a sami nasarar kammala kashe-kashen da ke cikin kwas cikin lokaci. Idan xalibi ya kammala karatu cikin lokaci, yana da damar sake bitar abubuwan da aka yi a baya kafin jarabawar qarshen zangon karatu.

Muhimman abubuwan da suka shafi wannan kwas sun haxa da:

a. Rarraba rukunin zuwa kashi – kashi (study units)
b. Manazarta da abubuwan kara nazari (reference)
c. Tambayoyi na auna fahimta (jinga). Assignment file
d. Tarin gabatar da Darasi (presentation schedule)

**Kashe-kashen Darasi (Study Units)**

Bayanai sun gabata waxanda ke nuna cewa wannan kwas HAU: 207 yana qunshe da kashi-kashi har guda goma sha shida. Ana bukatar a kammala kowane kashicikin sati guda ne wanda ya haxa harda amsa tambayoyi da ke qarshen kowane kashi da kuma amsa tambayoyin jinga idan akwai shi a qarshen darasin. Waxannan kashe-kashen su ne:

**Rukuni Na 1 Ma'anar Adabin Baka**

Kashi Na 1: Ma'anar Adabin Baka
Kashi Na 2: Rabe-raben Adabin Baka
Kashi Na 3: Bayani game da Waqar Baka na Hausa
Kashi Na 4: Bayani Game Da Zube na Baka
Kashi Na 5: Bayani Game Da Wasannin Kwaikwayo Na Baka

**Rukuni Na 2 Yadda ake Gane Adabin Baka Na Hausa**

Kashi Na 1: Yadda Tsari Yake
Kashi Na 2: Yin Amfani Da Harshe
Kashi Na 3: Aiwatarwa
Kashi Na 4: Ji Da Gani

**Rukuni Na 3 Yaya Ake Tattara Adabin Baka?**

Kashi Na 1: Matsalar Rashin Rubutu/Adana
Kashi Na 2: Wurin Masu Shekaru
Kashi Na 3: Kulawa Da Tanaden-tanaden Al'ada
Kashi Na 4: Yiwuwar Ragi ko Qari

**Rukuni Na 4 Hikimomin Zantukan Baka Na Hausa**

Kashi Na 1: Karin Magana
Kashi Na 2: Salon Magana
Kashi Na 3: Take Da Kirari
Kashi Na 4: Zaurance

**Manazarta da Abubuwan Qara Nazari**

A qarshen kowane kashi akwai manazarta wanda zai taimaka wa xalibai qara nazari da zurfafa bincike. Wasu daga ciki litattafai ne waxanda ba masu wuyar samu ba ne a xakunan sayar da littafai musamman waxanda ke sayar da na Hausa. Akwai littattafan adabin baka na Babajo A. K, (2011) da na Xangambo, (2008) da Okoh, (2008) waxanda ya kamata xalibai su nemo su don su qara karatu. Wasu kuma kundaye ne na kammala karatu digiri na xaya da na biyu har da digirin digirgir, wasu kuma muqalu ne ko dai a mujallu ko waxanda aka gabatar a tarurukan qara wa juna sani. Wasu daga ciki za a iya samunsa ta kafar sadarwa ta yanar gizo, ko kuma da taimakon xakunan karatu na Jami'o'i, musamman jamai'ar da take kula da "karatu daga gida" idan littattafan sun yi qaranci, ko kuma wuyar samu, to yana da kyau a yi amfani da bayanan da wannan manhajar kwas xin ya samar

**Auna Fahimta (Assignment)**

Gwaji da ake wa xalibai domin gane fahimtar su a wannan kwas suna kasancewa ta hanyoyi guda biyu ne. Hanya ta farko ita ce, ta ayyukan da ake ba xalibai su yi domin a gyara. Hanya ta biyu ita ce, wadda ake jarraba xalibai a qarshen zangon karatu (examination). Da yake yanzu komi na koyarwa sun koma ta na'urar mai qwaqwalwa ce, haka ma jingar da ake ba xalibai. Ana basu ne kuma suna amsawa da turowa nan take da zarar

sun gama amsa tambayoyin da aka yi masu. Daga ba tare da jimawa ba za su sami sakamakon jarrabawar da suka yi. Yana da kyau a kiyaye lokaci wajen amsa kowace tambaya domin yin haka kan taimaka wajen amsa tambayoyi duka cikin lokaci. Ana sa ran xalibai su amsa tambayoyin auna fahimta aqalla guda uku waxanda daga cikin ukun nan ne za a zavi qwarara guda biyu waxanda xalibi ya fi samun maki don su kasance kashi talatin cikin xari na jararrawa (30%), sauran kashi saba'in (70%) ana samunsu ne a jarrabawar qarshen zangon karatu (semester examination). Ita wannan jarrabawar zangon qarshen karatu, ana yin ta ne ta hanyar yanar gizo, saboda haka yana da kyau xalibai su kasance sun gwane da naqaltar na'urorin kwamfuta saboda a sami cin jarrabawa yadda ya kamata.

## Jinga (Tutor Marked Assignment)

Xalibai za su iya gwada fahimtarsu game da wannan kwas ta qoqarin amsa tambayoyin da ke qarshen kowane kashi. Dole kowane xalibi ya san manufar kowane kashi na darussan da suka gabata. Idan ya san haka ne zai iya gwada fahimtarsa ta hanyar amsa tambayoyin da ke biye a kowane kashi. Duk da cewa jarrabawar da ake ba xalibai ta yanar gizo suke, duk da haka xalibai za su iya gwada fahimtarsu ta qoqarin amsa tambayoyin da ke qarshen kowane kashi.

## Jarrabawa (Final Examination and Grading)

Ya kamata xalibi ya sani cewa jarrabawar qarshen zangon karatu na xaukar kashi saba'in (70%) cikin xari na sakamakon da ya kamata xalibi ya samu. Akan ciro tambayoyin da xalibai za su amsa daga cikin ire-iren tambayoyin da ake yi a qarqashin auna fahimta ta qarshen kowane kashi. Don haka yana da kyau xalibai su yi qoqarin amsa waxannan tambayoyin da aka yi masu a qarshen kowane kashi da aka gabatar, ana son a yi amfani da kyakykyawar Hausa da misalai masu kama hankali.

**MAIN COURSE**

## CONTENTS

**Rukuni Na 1 Ma'anar Adabin Baka**

Kashi Na 1: Ma'anar Adabin Baka
Kashi Na 2: Rabe-raben Adabin Baka
Kashi Na 3: Bayani game da Waqar Baka na Hausa
Kashi Na 4: Bayani Game Da Zube na Baka
Kashi Na 5: Bayani Game Da Wasannin Kwaikwayo Na Baka

**Rukuni Na 2 Yadda ake Gane Adabin Baka Na Hausa**

Kashi Na 1: Yadda Tsari Yake
Kashi Na 2: Yin Amfani Da Harshe
Kashi Na 3: Aiwatarwa
Kashi Na 4: Ji Da Gani

**Rukuni Na 3 Yaya Ake Tattara Adabin Baka?**

Kashi Na 1: Matsalar Rashin Rubutu/Adana
Kashi Na 2: Wurin Masu Shekaru
Kashi Na 3: Kulawa Da Tanaden-tanaden Al'ada
Kashi Na 4: Yiwuwar Ragi ko Qari

**Rukuni Na 4 Hikimomin Zantukan Baka Na Hausa**

Kashi Na 1: Karin Magana
Kashi Na 2: Salon Magana
Kashi Na 3: Take Da Kirari
Kashi Na 4: Zaurance

# KASHI NA 1: MA'ANAR ADABIN BAKA (ORAL LITERATURE/ORATURE)


**Abubuwan da ke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Ma'anar Magana
1.3.1 Ma'anar Zancen na Baka (Oral)
1.3.2 Ma'anar Zance a Rubuce (Literate)
1.3.3 Haxuwar Vangarorin Biyu (Orature)
Auna Fahimta na 1
1.4 Taqaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 1.1 Gabatarwa

Ga wanda yake son ya san ko ya fahimci ma`anar adabin bakan Bahaushe to sai ya fara da ma`ana. Ita kuma ma`ana ana iya kallonta ta vangarori guda uku: akwai ma`anar magana da kuma ma`anar zantuka na baka da kuma zance a rubuce. Daga nan ne wannan kwas zai bi diddigin bayani game da adabin bakan Bahaushe da yadda ake gane adabin da yadda ake tattara shi tare da kuma sauye-sauyen da ya samu daga lokaci zuwa lokaci.Xaya daga cikin hikimomin da Allah ya baiwa xan Adam wadda ta bambanta shi da dabbobi ko sauran halittu ita ce ta yin magana, magana kamar yadda za mu ga ma`anarta daga bakin masana ba ta wuce gurnani da motsi da baka wadda mutum ke yi don sadar da saqo ga xan uwansa ba. Akwai magana tsakanin mutum da mutum wadda ta shafi harkokin rayuwa wadda kowa na iya yinta, akwai kuma magana ta hikima da fasaha da ilimi wadda sai wanda yake da baiwa ta musamman zai furta ta. Saboda haka, ba kowace magana take adabin baka ba, amma duk adabin baka magana ce ta baka. Wannan darasi zai duba ire-iren magana da zantuka na baka da rubutacce domin gano matsugunin ko samuwar nazarin adabin baka ga al`ummar baqar fata musamman Hausawa.



## 1.2 Manufofin Darasi

A qarshen darasin, ana sa ran xalibai su gane:

a. Ma`anar magana
b. Zantukan na baka
c. Samuwar kalmar Adabin Baka (Orature)

## 1.3 Ma’anar Magana

A sauqaqe za a iya sifanta magana da cewa tsari ne na wasu gurnani masu ma`ana da mutane ke yi tsakaninsu don sada saqonnin da ke zukatansu game da duk wasu harkoki nasu na yau da kullum, babban abin da ya raba su da sauran hallitu. Sani, (2012:1). A Qamusun Hausa na Bayero (2006:316) an gwada cewa, Magana na nufin jerin kalmomi da aka furta da baki, kuma masu ma`ana. Abin da wannan yake nufi shi ne yin amfani da kalma ko kalmomi a matsayin wata hanya ta sadarwa tsakanin al`umma. Shi kuwa Abubakar, (2015:343), ya bayyana ma`anar magana da zancen da ake faxa da baka.

### 1.3.1 Ma’anar Zancen na Baka (Oral)

Zance ko zantuka na baka na nufin duk wasu zantukan magana waxanda aka furta su da baka, ba tare da an rubuta ba. Zance na baka na nufin magana da aka yi da baka, Idan haka ne, yana da kyau a fahinci cewa, ba kowane zance na baka yake iya zama adabin baka ba. Amma kowane adabin baka na iya zama zance na baka. Bambancinsu shi ne, shi zance na baka na iya kasancewa kowane irin zance, amma adabin baka zantukan hikima da fasaha ne waxanda suka xara zantuka na baka saboda akwai sarrafa harshe, akwai naqaltar harshe da qyale-qyalen jawo hankali da wasa da kalmomi a zantukan hikima na baka. Shi kuwa zance na baka ko magana ta baka ba ta buqatar waxannan qyale-qyalen.

### 1.3.2 Ma’anar Zance a Rubuce (Literate)

Idan an faxaxa ma`anar zantuka a rubuce, za a iya cewa sun qunshi duk wasu zantukan ko tunanin da aka yi amfani da alqalami aka rubuta su maimakon a furta su ta baka. Ashe duk wasu rubutu da aka yi waxanda suka shafi kiwon lafiya ko tarihi ko lissafi ko qere-qere duk zantuka ne a rubuce. Amma shi kuwa rubutaccen adabi (literature), zance ne a rubuce wanda ke xauke da hikima da fasahar al`umma. Kalmar **‘Literature’** ta samo asali ne daga kalmar latin **(littera)** wanda ke nufin harafi na rubutu, ko kuma jam`i **(litterae)** watau haruffan rubutu. Daga nan ne ake jin an sami kalmar **literature**, wato iya karatu da rubutu, waxanda suka iya wannan (karatu da rubutu) ana kiran su **literate**, saboda haka ba kowane zance a rubuce yake rubutaccen adabi (literature) ba.

### 1.3.3 Haxuwar Vangarorin Biyu (Orature)

Hausawa, kamar sauran al'ummomin Afrika sun daxe da hikimominsu da fasaharsu tun kafin su yi huxa da wasu al'ummomi ko qabilu, waxannan hikomomin da fasahar ana qirqirarsu a ka, a kuma adanasu a ka sa'annan a wanzar da su ta baka watau 'Oral'. Ana adanasu ne ta hanyar wanzarwa daga wancan zamani zuwa wannan bayan an haddace a kuma wanzar ta labartawa a duk lokacin da buqatar haka ta taso.

Kalmar 'Literature' mai nufin Adabi a Hausa, kalma ce mai buqatar kulawa ta musamman wanda za a yi bayani nan gaba. Qoqarin da ake yi a nan shi ne a fahimci cewa kalmar 'Oral' da 'Literature' su ne aka taqaita

aka fitar da kalmar 'ORATURE' watau a kalmar Oral aka fitar da Ora, a kalmar Literature aka datse gavovin farko aka xauki gava biyu ta qarshe 'ture' aka fitar da kalmar Orature mai nufin fasahar Adabin Baka.Idan dai wannan hikimar ake magana a kai, to ko shakka babu Bahaushe yana da ita wadda ya gada tun kaka da kakanni.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar magana da muhimmancinta ga rayuwar xan Adam.
2. Me aka fahimta da zantuka na baka? Ta yaya suka bambanta da adabin baka?
3. Bayyana yadda aka sami kalmar adabin baka (orature).



## 1.4 Taqaitawa

A wannan darasi, an yi bayanin ma`anar magana wadda take nufin gurnani na xan adam masu masu ma`ana, ita wannan magana tana xaya daga cikin abubuwan da suka bambanta mutum da dabba. Bayan nan, darasin ya bayyana ma`anar zance na baka da kuma rubutacce. An kuma gwada yadda harhaxuwar waxannnan kalmomi suka samar da adabin baka (orature).

Bayanai sun gabata wajen tabbatar da cewa ba kowane zance nab aka yake adabin baka ba. Amma kuma kowane adabin baka na iya kasancewa zantuka na baka ba don komai ba sai don zantukan an qirqire su a ‘ka’, aka kuma wanzar da su ta baka.

## 1.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Adabi: Zantukan da suka qunshi fusaha ko azanci a fannonin rayuwa daban-daban domin koya wani darasi ga al’umma, walau cikin furuci ko a rubuce.
- Qirqira: Gano hanyar yi ko samar da wani.
- Hikima: Yin wani abu da ya burge mutum.
- Magana: Jerin kalmomi da aka furta da baki kuma masu ma’ana.



## 1.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari


Abubakar A.T. (2015). Qamusun Harshen Hausa.Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Babajo, A. K. (2011). *Orature: Meaning, Nature and Forms*. A study Guide for Undergraduate Kaduna: Slimline Communication.

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Okoh, Nkem. (2008). *Preface to Oral Literature*, Africana First Publishers Limited, Books House Trust, Onitsha Nigeria.

Sani, M.A.Z. (2012). *Jagoran Nazarin Tsarin Sautin Hausa*, Kano: Usman Al`amin Publishers.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Bayyana ma'anar magana da muhimmancinta ga rayuwar xan Adam.
A sauqaqe za a iya sifanta magana da cewa tsari ne na wasu gurnani masu ma`ana da mutane ke yi tsakaninsu don sada saqonnin da ke zukatansu game da duk wasu harkoki nasu na yau da kullum, babban abin da ya raba su da sauran hallitu.
2. Me aka fahimta da zantuka na baka? Ta yaya suka bambanta da adabin baka?
Zance ko zantuka na baka na nufin duk wasu zantukan magana waxanda aka furta su da baka, ba tare da an rubuta ba. Bambancinsu shi ne, shi zance na baka na iya kasancewa kowane irin zance, amma adabin baka zantukan hikima da fasaha ne waxanda suka xara zantuka na baka saboda akwai sarrafa harshe, akwai naqaltar harshe da qyale-qyalen jawo hankali da wasa da kalmomi a zantukan hikima na baka. Shi kuwa zance na baka ko magana ta baka ba ta buqatar waxannan qyale-qyalen.
3. Bayyana yadda aka sami kalmar adabin baka (Orature).
kalmar 'Oral' da 'Literature' su ne aka taqaita aka fitar da kalmar 'ORATURE' watau a kalmar Oral aka fitar da Ora, a kalmar Literature aka datse gavovin farko aka xauki gava biyu ta qarshe 'ture' aka fitar da kalmar Orature mai nufin fasahar Adabin Baka.Idan dai wannan hikimar ake magana a kai, to ko shakka babu Bahaushe yana da ita wadda ya gada tun kaka da kakanni.

## Kashi Na 2: Rabe-Raben Adabin Baka: Bayani Game da Waqar Baka

### Abubuwan da ke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Ma’anar Waqar Baka
2.3.1 Ma’anar Makaxan Baka
2.3.2 Rabe-Raben Makaxan Baka na Hausa
2.1.2.1 Makaxan Fada
2.1.2.2 Makaxan Kowa da Kowa
2.1.2.3 Masu Kixan Maza
2.1.2.4 Kaxe-Kaxen Mata
2.1.2.5 Makaxan Ban Dariya
2.1.2.5 Makaxan Zamani
2.2 Ire-iren Kayan Kixa
2.2.1 Nau’o’in Ganguna
2.2.2 Waxanda ake Busawa
2.2.3 Nau`in Isga da Tsakiya
2.2.4 Sauran Kayan Kixa
2.2.5 Kayan Kida Na Zamani
2.3 Manufar Waqoqin Baka
2.3.1 Yadda ake Wanzar da Waqoqin Baka
2.1.3 Tsarin Waqoqin Baka
2.3.2 Sarrafa Harshe a Waqoqin Baka
Auna Fahimta na 1
2.4 Taqaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 2.1 Gabatarwa

Darasin da ya gabata, ya bayyana wa mai karatu ma`anar magana da kuma yadda magana take a baka da rubutatta, da yadda aka samu adabin baka. A wannan kashin za a yi bayanin rabe-raben adabin baka musamman waqar baka da zube na baka da kuma wasannin kwaikwayo na baka, ba a nan abin zai tsaya ba, har da bayanin zantukan hikima waxanda suka kasance cikamako na adabin baka.

Ke nan idan aka natsu aka yi nazarin wa}a a zahiri za a ga wani zance ne ko magana da ake ta ja har ta yi tsawon gaske. Amma ga masana wa}a na nufin abubuwa da yawa.Ga [angambo, (2007) wa}a na nufin sa}on da aka gina bisa tsararriyar }aida ta baiti ko ]ango ta hanyar rerawa da kuma samun kari ko bahari da amsa amo ko }afiya. Ke nan za a iya cewa wa}a ta bambanta da zance na yau da kullum ta fuskar tsarawa da }a’idoji.

Ita wa}ar baka ita ce wadda mawa}an baka irin su Shata da [an}wairo da Choge mai Amada kan yi. Haka akwai wa}o}in baka na dandali da 'yan mata da na da~e da daka da sauran su.Mu xauki waqar baka, wato waqar da ake qagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka. Za a tattauna musamman abin da ya shafi ma'anar waqar baka da makaxan baka, sai kuma ire-iren waqar baka da kayan kixan Hausawa na gargajiya da na zamani. Sa`annan kuma kashin ya qunshi bayani kan turke da salo da tsarin waqar baka. Za a tattauna musamman abin da ya shafi ma'ana da yadda turke da salo da tsari yake a waqar baka.

## 2.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da waqoqin baka na baka na Hausa da ire-irensu. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai za su fahimci ma'anar waqar baka da makaxan baka da rarrabe waqar baka da makaxan baka, hatta Ire-iren makaxan baka da kayan kixansu.

## 2.3 Ma'anar Waqar Baka

Kafin a tsunduma kan ma`anar da masana suka gabatar, yana da muhimmanci a gane abin da kalmar wa}a ke nufi ga mutumin da ya tashi a }asar Hausa. Idan ka ha]u da mutum a kasuwa ko bakin titi ko a wani wuri na gargajiya ka tambaye shi abin da ake nufi da wa}a da Hausa abin da zai iya fa]a maka ba zai wuce, 'yawan son yin abu ba' ko kuma 'jan magana ko nanata zance kan wani batu da ake son yi.' Shi ya sa za ka ji mutum na cewa kullum ina wa}ar zan zo mu gaisa amma abin ya faskara. Ma'ana yana ta sa}ar zuci na son zuwa inda wancan aboki yake, amma bai je ba. Ke nan wa}ar abu na nufin ka yi ta kururuta batu ko jan batun a zuci na tsawon lokaci, amma ba aikatawa.

Masan da dama sun yi bayanin ma`anar waqar kwatankwacin yadda suka fahimce ta. Abubuwan da ya kamata xalibi ya gane a nan sun haxa da siffofin waqar baka , wato rerawa da baki da haxe da kixa da rawa wani lokaci da `yan amshi. Bari dai mu ga abin da shaihunnan malamai suka ce game da ma`anar waqar baka. Waqoqin baka kamar yadda sunansu ya nuna, su ne waqoqin da aka yi da baki, abin nufi a nan shi ne, su dai waqoqin baka shirya su ake yi a zuci, kuma a gabatar wa mutane da su ta hanyar rera su da baki. Tun ainihinsu ba a rubuce suke ba, kuma mawaqan da suke tsara su, ba a rubuce suke tsara su ba, sun vullo da su ne ta hanyar rerawa da baki, wani lokaci tare da kixa, wani lokaci kuma babu, (Tsoho, 1983:1). Waqoqin baka sun qunshi waqoqin mata na aikace-aikacen cikin gida da waqoqin yara na dandali da waqoqin cikin tatsuniyoyi da kuma waqoqin makaxa da mawaqan Hausa na gargajiya. Gusau (1984), ya bayyana waqar baka da cewa; "wani saqo ne cikin zance da azanci da ake rerawa ba faxa kurum ba, ta hikima da fasaha da zavavvun kalmomi waxanda suka dace da saqon, kuma tana zuwa gunduwa-gunduwa da sautin murya da kixa da armashi da gaxa da tafi mai saka zuciya jin daxi."

(Gusau, 2008), ya qara da cewa akwai wasu matakai wato kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma'anar waqar baka, waxannan kalmomi sun haxa da rerawa da hawa da saukar murya da daidaita murya da rauji da naqaltar harshe da hikima da fasaha da kixa da karvi ko amshi.

### 2.3.1 Ma'anar Makaxan Baka

Akwai makaxa iri daban-daban, rabe-raben makaxan, ya dogara ga irin waqoqin, da kuma dangantaka da dalilan da suka sa ake yin waqoqin da kaxe-kaxen da irin mutanen da ake yin waqoqin dominsu.A cikin waqoqin baka na Hausa akwai waxanda ba a gwama su da kixa misali, waqoqin raino ko na aikace-aikacen gida na mata ko waqoqin dandali. Su waxannan waqoqi suna samun amo ne daga tafi ko sautin kayan aikace-aikacen da sauransu. Akwai kuma waqoqin baka na makaxan baka waxanda ake gwama su da amo na kixa da kayan kixa. Waxannan kalmomi guda biyu, makaxa+ baka, suna yin nuni ne dangane da mutanen da suke yin kixa da waqa, amma da fatar baki. Ma'anar kixa a nan za ta iya zama yin waqa tare da kaxa ko buga wani abu mai ba da amo ko sauti. (Gusau, 2008:110)

### 2.3.2 Rabe-Raben Makaxan Baka na Hausa

Rarraba makaxan baka na Hausa ba abu ne mai sauqi ba, amma idan aka yi la`akari da saqonnin waqoqinsu ko ta fuskar kayan kixansu ko kuma ta fuskar waxanda suke yi wa waqoqinsu za a iay rarraba su. Idan an bi ta waxanda makaxan suke yi wa waqoqinsu, akwai makaxan fada da makaxan jama'a da makaxan maza da makaxan mata da makaxan ban dariya da sauransu.

#### 2.3.2.1 Makaxan Fada

Da jin an ce fada, abin da zai zo ma mai karatu rai shi ne Sarauta. Sarauta kuwa na samuwane sanadiyyar kafa Daula ko gari ko masarauta, inda wasu daga cikin al`umma kan shugabanci jagorancin mutane. Su waxannan shugabanni suksn kasance tare da masu yi masu hidima da aikace aikace waxanda suka haxa har da makaxa. Makaxan fada makaxa ne da suke waqoqin fada ko na sarauta. Irin waxannan makaxa ba sa yi wa kowa kixa da waqa, in ba basarake ba. Akasarinsu suna da ubangida basarake wanda shi kaxai suke yi wa kixa da waqa. Ko da za su yi wa wani wanda ba ubangidansu ba waqa, sai sun nemi izini daga iyayen gidan nasu. A taqaice dai, makaxan fada su ne waxanda suke yi wa sarakuna da hakimai da dagatai da manayan fadawa da masu riqe da sarautun gargajiya da duk wanda ya danganci jinin sarauta ko kuma yake riqe da wani muqami na sarauta waqoqi. (Gusau, 2008:138). Misalin makaxan fada sun haxa da, Alhaji Musa Xanqwairo Maradun da Ibrahim Narambaxa da Salihu Jankixi Sarkin Taushi da sauransu.

#### 2.3.2.2 Makaxan Kowa da Kowa

Ko da jin sunan ma an san irin waxannan makaxa suna yi wa kowa da kowa waqa, su waxannan makaxan ne ake kira da makaxaan jama`a. Ire-iren waxannan makaxa suna yi wa kowa da kowa waqa, walau sarki ko attajiri ko ma'aikata ko malamai ko jama'a gama-gari, da sauransu.

Misalan makaxan jama'a su ne Alhaji Mamman Shata Katsina da Alhaji Adamu Xan Maraya Jos da Hamza Caji da Garba Liyo da Ahmadu Doka da Alhaji Shehu Ajilo Xanguzuri da sauransu. Suna amfani da kayan kixa kamar kalangu da kuntigi da gurmi da goge da sauransu.

**2.3.2.3 Masu Kixan Maza**

Maza a wannan bigire na nufin waxanda suka yi fice da shahara a wata sana`a ko bajinta ta musamman, su irin waxannan mutane suna da masu yi masu kixa na musamman. Makaxan maza ko makaxan jarunta su ne makaxan da suke yi wa jaruntaka da jarumai kixa da waqa. Waxannan sun qunshi waqoqin varayi da waqoqin yaqi da waqoqin dambe da sauransu. Misalan makaxan maza sun haxa da Alhaji Muhammadu Gambo Fagada Mai Waqar Varayi da Xan'anace mawaqin dambe da sauransu.

**2.3.2.4 Kaxe-Kaxen Mata**

Ya kai mai karatu, ka lura fan au`o`in da ake Magana a nan ba matan ne ake wa kixa ba, a`a illa cewa nau`in kaxe-kaxe ne waxanda mata ke yi. Ire-iren kaxe-kaxen mata sun haxa da kixan gaxa da kixan shantu da kixan kalangu na saran marke da kixan duma wanda ake kaxa wa samari da 'yan mata da kixan dutsi da kixan qwarya. Baya ga waxannan kaxe-kaxe, akwai wasu mata da suka zama makaxa waxanda suke amfani da kixan qwarya da kixan ganga da kixan buta da kixan fiyano da makamantansu. Akwai kuma waqoqin mata maroqa irin su Barmani Coge da Uwaliya Mai Amada da sauransu. Sauran Waqoqin Mata sun haxa da waqoqin niqa da waqoqin reno da waqoqin talla.

**2.3.2.5 Makaxan Ban Dariya**

Akwai a cikin al`umma makaxa waxanda suka bayar da rayuwarsu wajen kixa domin sub a mutane dariya su cusa masu annashuwa da farin ciki da far`a. Duk da yake ana ba su `yan kuxaxe, amma dai bag a kixan kawai aka sansu ba, maqale da kixan akwai wata baiwa ta sa nishaxi cikin zukatan al`umma. Ire-iren waxannan makaxan ban dariya sun haxa da 'yan kama da 'yan gambara da makamantar waxannan.

**2.3.2.6 Makaxan Zamani**

A vangaren makaxan baka ma, akwai wanxanda suka samu saboda sauyin zamani, su waxannan makaxan zamani ne ya haifar das u da ire-iren waqoqin da suke yi. Dazamani ya shigo, wasu abubuwa sababbi sun bayana a tsarin waqoqin baka na Hausa.An bayyana cewa a vangaren waqoqin samartaka ne zamani ya shigo da tasirinsa a cikin waqoqin Hausa, wato waqoqin da samari da 'yammata ke yi(Gusau, 2008 : 345-360). Waqoqin zamani sun kunno kai gadan-gadan ne a tsakiyar qarni na ashirin (Q20) zuwa qarshensa , wato bayan yaqin basasa, lokacin da qabilun kudanci Nijeriya suka yawaita (varko) arewa da kuma yawaitar otel-otel a manyan garuruwan arewa. Tun a wajen shekara ta 1980 aka sami wasu makaxa waxanda suka dinga rera waqoqin Hausa ta amfani da kayan kixa baqi. An sami makaxa irin su Bala Miller da Fumi Adams da Audu Kwarisko da Sa'adu Bori da sauransu. (Gusau, 2008: 348). A wajen shekara ta 1995 wasu Hausawa,

musamman samari, suka fara tsara waqa a rubuce sannan su samar mata rauji, su kuma rera ta amfani da kayan kixa baqi. Wasu su haddace waqoqin da ka, wasu su ajiye su a kasa-kasai da CD – CD. Zuwa shekara ta 2000 jama'a ta fara sabawa da waxannan kaxe-kaxe na fiyano da ake tsarmawa a cikin fina-finai. (Gusau, 2008:349). Yawancin irin waxannan mawaqa idan suka zo maimaita rera waqoqin suna bin rerawa ta farko ne daga CD wanda aka riga aka naxa a sitidiyo, abin da ake kira '*Mamming*' da Ingilishi. Wannan kai tsaye tasiri ne baqo wanda Hausawa suka samo shi daga tsari na naxar waqoqin Turawa. Ga abin da Alan Waqa yake cewa game da wannan:

"Baituka na zo in yi da kixa na Nasaranci,
Kun ga na yi gurmi da kixa na Yahudanci,
Baituka da sauti da salon masu Hausanci,
Yakana na taso in gwada da badangalci,
Ibrahimu za mu taya godiyar Allah."

(Aminu ALA: Waqar *Farfesa Malumfashi*).

A yawancin lokuta, karin murya da saqon iri xaya ne da na waqoqin Sa'in na asali, sai dai sukan bi wasu salo na zamani wajen tsara waqar da kuma gwama su da kixa na zamani.(Mujaheed, 2018). Makaxan zamani sun qunshi Aminu Alan Waqa da Adam A. Zango da Fati Nijar da Dauda Kahutu Rarara da sauransu.

### 2.2 Ire-Iren Kayan Kixa

Gwama wasu abubuwa waxanda za su bayar da wani amo na musamman ko sauti na musamman shi ake kira da kixa.Misali gwama baki+qahon dabba, ko dutse+dutse, ko tafi+tafi, ko ganga + gula ko makaxi da sauransu suna samar da amo ko qara da ake bukata, sarrafa wannan qarar don ta dace da bukatar da ake da ita aiki ne na makaxi. Haka kuma duk da yake ana yin kixa don wata manufa, kixa yakan shiga jikin mai sauraro, ya sa masa karsashin da har za ta kai shi ya dinga rausayawa yana tattakawa. (Gusau 2008:54).

#### 2.2.1 Nau`o`in Ganguna

Su ne waxanda ake kaxawa da hannu ko ta amfani da gula wato xan makaxi. Sun qunshi;

**Ganga-** Wannan babbar ganga ce wadda ake yi wa babban maratayi. Yawanci ana amfani da ganga wajen qixan noma ko na aikin gayya. Akan kuma sami wani nau'i na ganga qarama wadda wasu suke kira farar ganga.

**Kalangu-** Abin kixa ne wanda ake ratayawa a kafaxa ana bugawa. Kalangu nau'i biyu ne: akwai babba da qarami. Ana iya kixa babban kalangu shi kaxai ba tare da haxa shi da wani abin kixa ba. Amma qaramin wanda ake kira kazagi ko kauzagi yakan zama mahaxi ne na babban kalangu ko wani abin kixa kamar duma. Makaxan sukan xaura shi a cinya yayin da suke buga babban abin kixa.

**Duman Girke-** Ana yin duman girke ne da duma manya da matsakaita masu bi wa juna a tsayi da faxi. Ana kaxa su domin a yi rawa kawai

amma banda waqa. Makaxansu na jera su a gabansa ya riqa bugawa. Kowannensu na bada sauti irin daban.

**Kotso-** Qaramar ganga ce. Sannan tsakiyar kotso a tsuke take, sa'annan kotso na da buxaxxen baki domin ya ba da sauti mai zaqi.

**Tambari-** Wannan babbar ganga ce mai shige da qwarya. Tambari ganga ce ta sarakai kawai. Hausawa sun samo ta ne daga al'ummar Barebari.

Sauran kayan kixa nau'in ganguna sun haxa da:

| | |
|---|---|
| Turu | Jauje |
| Talle | Dundufa |
| Kurya | Banga |
| Zakka Tallabe | |
| Qoroso | bandiri/mandiri |
| Kwairama | Kuwaru |
| Duma | Cali |
| Taushi | Kotso, da sauransu |

### 2.2.2 Waxanda ake Busawa

Kayan busa su ne waxanda ake amfani da su ta hanyar busawa, su ne:

**Algaita:** Algaita abin busa ne, saraki ake yi wa busar algaita.

**Farai:** Farai ma abin busa ne, kuma kamar algaita, farai kixan saraki ake yi da shi, tun ma ba Sarkin Musulmi ba.

**Qaho:** Qahon da aka fi amfani da shi wajen busa shi ne qahon saniya ko bajimin sa. Ana yi masa qofofi guda uku, xaya babba daga sama gefen dama, xaya kuma qarama daga gindinsa, da kuma wadda za a yanka daga tsakiya a dinga sa baki ana busawa. Ana tattava sauran qofofin da hannu.

**Kakaki:** Kakaki abin busawa ne. Ana yin sa ne da qarfe mai kama da saholama. Nau'i biyu ne qarami marar faxin ciki wanda za su yi wa qofa, da babba mai xan tsawo da faxin ciki. Wani lokaci ma akan yi shi gaba uku yadda za a iya kakkarya shi. Daga nan, za a yi qofa qarama daga gindinsa (farko) inda za a sa baki a dinga busawa da qofa babba daga qarshensa wurin da sauti zai dinga fita.

Sauran kayan bushe-bushe sun qunshi:

| | |
|---|---|
| Sarewa | Damalgo |
| Qwabiri | Siriqi |
| Kwagira | Kulema |
| BututuFamfami | |
| Tilliveri | Usur, da sauransu. |

### 2.2.3 Nau`in Isga da Tsakiya

Su ne waxanda ake kaxa su ta hanyar goga tsarkiya da ke jikinsu, misalansu;

**Goge:** Goge ana goga shi ne. Ana amfani da izgar doki wajen qulla abin da ake gogawa.

**Kukuma:** Kukuma kamar goge yake sai dai sautinta ba iri xaya yake da na goge ba.
**Garaya:** Wannan abin kixa ne da ake kaxawa an fi amfani da garaya wajen kixan bori ko na iskoki.
**Kuntigi:** Kuntigi shi ma kaxa shi ake yi amma girmansa bai kai na garaya ba.
**Gurmi:** Gurmi ya xara kuntigi tsawo, shi ma ana kaxa shi ne kamar garaya ko kuntigi.
**Molo:** Molo ya yi kama da kuntigi ko garaya amma ya xara su girma. Shi ma kaxa shi ake yi kuma ana haxa shi da qoqo da duma.
Wasu daga cikin kayan izga da tsarkiya sun haxa da:
Kumsa
Kumbo
Gyanxama, da sauransu.

### 2.2.4 Sauran Kayan Kixa

Wato kayan kixa da ba na bushe-bushe ba, ba kuma ganguna ba. Amma ana amfani da su wajen samar da amo na kixa. Ire-iren waxannan kayan kixa sun haxa da:

Shantu Ruwan fartanya
Xuwawu
Kuje Cekki
Qwarya
Buta Zunguru
Saqa
Barancaki Tasa da sauransu
Kacau-kacau Gora
Sakaina Madavi
Zuga-Zugai Dutsen niqa
Gwangwani Turmi
Akayau Tafin hannu, da sauransu.
Sakaina Qwarya, ko Akayau.
Shantu ko Bambaro ko Barakaci.

### 2.2.5 Kayan Kida Na Zamani

Kayan kixa na zamani baqi ne a qasar Hausa. Wato salon waqoqin zamanin ya haifar da samuwar kayan kixan zamani da suka haxa da fiyano da jita da tasoshi da sauransu.

## 2.3 Manufar Waqoqin Baka

Makaxa na shirya kalmomi su haxa su da amon kixa su rera ta amfani da wani rauji tare da sakaxa wani saqo ko tuke domin isar wa al'umma (Gusau, 1993).Makaxi kan yi kixa da waqa mai xauke da saqonni da dama.

Muhimman manufofin da za a iya ji ko hararowa daga waqoqin da makaxan baka na Hausa suke shiryawa sun haxa da kira da a riqe al'adu masu kyau, sannan kuma suna qoqarin dakushe marasa kyau. Daga cikin turaku na waqoqin baka, akwai;

i. **Wa'azantarwa:** Yawanci makaxan baka, musamman na da, sukan yi waqoqi don yi wa al'umma wa'azi na horo da hani. Misali, Alhaji Mamman Shata Katsina ya yi wa mata wa'azi da su dinga yin aure. A wasu xiya na waqar yana faxin:

Jagora: Don Salla da salatil Fati,
: Albarkar girman mai girma,
'Y/Amshi: Don Salla da Salatil Fati,
: Kai don Allah mata ku yi aure.

ii. **Ilmantarwa da Wayar da Kai:** Makaxan Hausa suna yin wasu waqoqi domin ilmantar da mutanensu da kuma wayar masu da kai kan wasu al'amura da ba su fahimta ba. Alal misali, a lokacin da aka sauya kuxi a Nijeriya zuwa Naira da Kwabo. Makaxa Haruna Uje ya yi waqa don wayar wa al'umma kai game da sababbin kuxin. Daga cikinta yana cewa;

Jagora: Naira da kwabo sabon kuxi,
: Daxa kun ji kuxin Nijeriya,
: Allah qaro mana arziqi,
: Gami da wadatar duniya.
Jagora: Idan ba ka san su ba,
: Jikin Naira Biyar,
: Fentinta da kore xan kaxan,
: Kuma ka ga mutum guda.
Jagora: Da singileti wuya,
: Ka gane shi a durqushe,
: Hannunsa akwai adda riqe,
: Yana ta aikin kwakwan nan ta manja.
(Haruna Uji: Waqar *Naira da Kwabo*).

iii. **Faxakarwa:** Makaxan Hausa, mutane ne waxanda suke yi wa al'ummarsu faxakarwa game da al'amuran rayuwa ta hanyar yi masu hannunka mai sanda da gargaxi da tunasarwa da sauransu. Alhaji Mamman Shata Katsina ya yi wa mutanen Arewa gargaxi da su tashi su nemi na kansu, su daina zaman banza da bacci domin ayyuka ne na lokaci. A wasu xiya ana cewa:

Jagora: Kai mai aski tsare askin naka,
: Mai tebur tsare kan teburinka,
: Mai akwaku tsare kayanka,
: Mai noma ka tsare gonarka,
: Ku turu mu farka xiyan Arewa,

: Ku san barci aikin kawai ne,
'Y/Amshi: Mu Tashi mu farka 'yan Arewa
: Mu san Barci aikin kawai ne.
Jagora: Kun ji ku tashi ku farka 'yan Arewa,
: Kowane aiki mutum yake yi,
'Y/Amshi: Mu tashi mu farka 'yan Arewa,
: Mu san barci aikin kawai ne.
(Shata: Waqar *Gargaxi ga 'yan Arewa*).

**iv Yabo:** Makaxan Hausa na faxar kalmomi masu daxi ga wanda ya aikata wani kyakkyawan abu. Ta yin haka suna fito da halaye da al'adun al'umma kyawawa. Wannan shi ne yaba hali, ko xabi'a na mutum ta nuna fara'ar mutum ko kyauta ko alheri ko adalci da rashin nuna bambanci tsakanin jama'a da sauransu. Misali, Shata ya yi wa Alhaji Sambajo waqa ta yabo inda ya fito da halayensa kyawawa da alheri da kyautarsa. A cikinta yana cewa;

Jagora: Ai ma fara'a ai ma alheri,
: kana a ja ka da wasan dangi,
: Je ka wurin Salisu Sambajo,
'Y/Amshi: Na gode wa Haji Sambajo.
Jagora: Kai mu je ko babu kixa ba waqa,
: Mu zauna nan mu yi wasan dangi,
'Y/Amshi: Na gode wa Haji Sambajo.
(Shata: Waqar *Salisu Sambajo*).

**V. Zuga:** Zuga tana xauke da wasu kalmomi ne da ake amfani da su a koxa wani mutum, a cicciva shi, a nuna fifikonsa kan wasu. Zuga takan tsuma mutum ta sa masa kuzari da qwarin gwiwa. A wajen zuga mutum akan yi amfani da kalmomin wasawa ko kumburawa ko ban tsoro ko ciccivawa ko razanawa ko fifitawa ko naqastawa da tauye zangon daraja da sauransu. (Gusau 2008:377). Misali

Allah ya yo ma xaukakad,
Da kowa ba shi da ita Hausa dut
(Xandawo: Waqar *Mai Yawuri Bangon Duniya*).

**Vi. Zambo**: Zambo kalma ce da ake amfani da ita a matsayin kishiyar yabo. Akan siffanta mutum da wasu siffofi munana waxanda za su wulaqanta shi ko su jawo masa rashin martaba a idon mutane, tare da kau da kai wannan mutum yana da waxannan siffofi ko ba shi da su. Akan qara gishiri a zambo don a daxa lalata hali ko xabi'ar wanda ake yi wa shi. (Gusau 2008:380). Misali

To bismilla Allah ta'ala,
Ga farillin malan na baya,
Ga tarihin malam na baya,
Aura dillalin quli-quli
(Xanmaraya Jos: Waqar *Karen Mota*).

**Vii. Siyasa:** Siyasa hanya ce wadda ake amfani da hankali da lafazi mai daxi a jawo ra'ayin mutane zuwa ga kyautata rayuwarsu. (Gusau,

2008). Yawancin waqoqin baka da aka shirya na siyasa sun danganci nuni kan kishin kai ko kishin qasa wani lokaci ma har da kishin addinin Musulunci. Wasu waqoqin kuma ana yi wa 'yan siyasa ne. misalan waqoqin da suka danganci turken siyasa sun haxa da;

- Babbar qasar Xanfodiyo Jamhuriyar Nijeriya.
  (Xanharxo Gumel: Waqar *Kishin Qasa*).

- Duniya ta yi kyau arziki ya yi,
  Tun da mun karvi 'yanci cikin sa'a.
  (Muhammadu Sarkin Taushi: Waqar 'Yancin Arewa 1959)

(Gusau, 2008: 382).

**Viii. Soyayya:** Akwai waqoqin baka waxanda suka jivinci turken saoyayya kamar waxannan;

- Allah Sarki ya Allah,
  Allah kai ni, Kaduna.
  (Haruna Uji: Waqar *Jummai*).

- Sai wata rana,
  Habibu sai wata rana,
  Na tuna da ran bankwananmu,
  Habibu sai wata rana.
  (Uwani Zakirai: *Bankwana da Masoyi*).

(Gusau, 2008: 383-384).

Waxannan su ne muhimman turakun waqoqin baka na Hausa duk kuwa da akan sami wasu saqonnin kamar na addini ko nishaxantarwa ko xarsashin zuciya ko jaruntaka da sauransu da yawa.

### 2.3.1 Yadda ake Wanzar da Waqoqin Baka

Wanzarwa a nan na nufin aiwatar da abu cikin tsari domin saqo ya isa ga mai saurare, xaya daga cikin hanyar da ake wanzar da waqoqin baka ita ce ta yin amfani da salon da ya dace. Ma`anar salo ga masana salo, bata wuce dabaru na isar da saqo cikin armashi ba, salo dabara ce wadda ake kyautata harshen waqa da ita tare da qawata zaren tunani ta yadda za a sarrafa shi cikin azanci ta zaven kalmomi ko sakaya furuci, a isar da saqo wanda ake ginawa ta hanyar kaifafa tunani da balaga mai armashi. Ke nan, salo a waqoqin baka wata hanya ce wadda makaxi ke kyautata zaren tunaninsa, ya sarrafa shi cikin azanci don ya cim ma burinsa na isar da saqo a waqa. (Gusau, 2003:54). Ya qara da cewa salo a waqoqin baka abu ne wanda yake daxa fito da ainihin kyansu ko muninsu, ta haka za a iya gane waqoqi masu karsashi, masu hikima da balaga da kuma waqoqi marasa ma'ana, marasa inganci. Salo kenan ma'auni ne na rarrabe zaqin

waqa ko xacinta. Salo kuma hanya ce ta sarrafa harshe a jujjuya shi ta yadda za a iya taqaita manufa ko a sakaya ma'ana ko kuma a kaifafa tunani, salo xaya ne daga cikin hanyoyin da ake bi wajen wanzar da waqoqin baka.

### 2.3.2 Tsarin Waqoqin Baka

Baya ga salo, akwai kuma wata siffa ta adabin baka, wannan siffar kuwa ita ce ta tsari. An bayyana tsarin waqar baka a matsayin awon waqar baka, da irin yadda ya shafi yadda makaxi yake shirya waqa a cikin zubin xiya da dabarun karin murya. Haka nan kuma an qara da cewa, a wannan vangaren, ana duba zubin layuka da yawan xiyan waqa da tsarin rerawa da karin murya da amsa-amon kari da sauran abubuwan da suka shafi awon baka. Xiyan waqa kuwa tamkar rassa ce ta itaciya wadda ake fara hawowa daga gindi kuma a sauka ta qasa. A kowane xa za a sami hawa da sauka. Ta haka ne mai nazari zai kula da yadda makaxi ya qulla carbin tunaninsa da yadda yake saqa kalmomi da saqonni cikin jimlolibaki xaya (Gusau, 2003:32-34).

Wani manazarcin kuma ya bayyana "tsari a nazarin waqar baka a matsayin fannin da ke fayyace xan waqa a matsayinsa na qunshiyar saqo ko manufa a cikin waqa da ke bayyana yadda mawaqi yake shirya tunaninsa wajen qulla kalmomi da jumloli su bayar da saqon da yake burin isarwa ga al'umma, Satatima, (2009:127-128).

Saboda haka, tsari a waqar baka na bayyana Rukunin da mawaqi ke amfani da shi wajen bayyana dangantakar da ke tsakanin xa da manufa wajen isar da saqo ta amfani da salo mai gamsarwa wajen rera waqoqi. A dunqule, tsari a waqar baka shi ne hanyar da mawaqi ya bi wajen jera tunaninsa tare da shirya shi domin ya isar da saqonsa ga mai sauraro, wajen tsari ya bambanta daga mawaqi zuwa wani mawaqin.

### 2.3.3 Sarrafa Harshe a Waqoqin Baka

Sarrafa harshe na nufin yadda aka yi amfani da harshe bisa qa`ida ko akasin haka, manufa ana mawaqi na iya bin dokokin nahawun harshe wajen gabatar da waqarsa, haka nan kuma yana da dammar karya qa`idar nahawu a yayin da yake waqarsa. Babu matsala ga wannan karya qa`idar matuqar dai ba ta sauya saqon da ake bukatar iosar wag a jama`a ba.Muhammad (1973), ya bayyana cewa salon sarrafa harshen waqa ya qunshi abubuwa ne kamar qarangiya da amsa-amo da xinkin baitoci da zambo da baqin kalmomi da Hausantarwa da tsofaffin kalmomi da karin harshe da savi-zarce da kuma wasu vangarorin adon harshe kamar su kwalliya da tamka da mutuntawa da kamance da kuma siffantawa. Xangambo, (2007) ya qara da ginin jumla da kuma nau'o'in jumla, sai dai kuma shi ya kira sarrafa harshen waqa da 'nahawun waqa'.

Shi kuwa Gusau, (2003:62-63) ya nuna cewa dangane da aiwatar da harshe a nazarin waqoqin baka akan duba hanyoyin zaven kalmomi da karin harshen waqa da kuma ginin jumla da tsarinta. Gusau, (2003:54), ya ci gaba da cewa za a iya karkasa salon sarrafa harshe zuwa gidaje biyu wato adon harshe da kuma aiwatar da harshe.Garba, (2011:45-46) ya

bayyana cewa; "Salon sarrafa harshen waqa ya qunshi abubuwa masu yawa waxanda suka haxa da qarangiya da amsa-amo da tamka da mutuntarwa da kamance da xinki da zambo da kwalliya da baqin kalmomi da Hausantarwa da karya dokar nahawu da karin harshe da savi-zarce da siffantawa. Sai a qara da sifar harshe wato ginin jimla da tsarinta da nau'o'inta, da yawa daga cikin masana suna ganin armashin waqa ko rashinta.

**Auna Fahimta**

1. Yi bayani ma`anar waqar baka.
2. Yi bayani kan biyar daga cikin kayan kixan Hausawa tare da misalai.
3. Mene ne tsarin waqar baka na Hausa ya qunsa?

## 2.4 Taqaitawa

Muhimman abubuwan da aka tattauna a wannan kashi su ne ma'ana da ire-iren makaxan baka da kayan kixansu na da, da na zamani. Kashin bai tsaya nan ba sai da ya duba turaku da salo haxe da tsari na waqar baka. Waqar baka kamar kowane nau'in adabi qunshe take da manufofin da ake fatar isar wa jama`a ta hanyar wanzar wa da sarrafa harshe cikin tsari na musamman. Shi ya sa a wannan kashi aka tattauna yadda manufa (saqo) yake a waqoqin baka tare da misalansa, sai kuma salo da sarrafa harshe da kuma a tsari a waqoqin baka na Hausa.

## 2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Saqo: Aike na magana ko kaya daga wani wuri zuwa wani.
- Salo: Yayi ko sauyi ko launi ko fice
- Zambo: Qaga wa mutum magana wadda za ta muzanta shi, ko ta vata masa suna.
- Nahawu: Qa'idojin sarrafa harshe

## 2.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa Na Qara Nazari

Xangambo, A. (2007). Xaurayar Gadon Fexe Waqa. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Garba, S. (2011). "Salon Sarrafa Harshe A Waqoqin Aqilu Aliyu". Kundin Digiri na Uku. Zariya: Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Gusau, S.M. (2008). *Waqoqin Baka A Qasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu.* Kano: Benchmark Pulishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). Diwanin Waqoqin Baka: Zavavvun Matanoni Na Waqoqin Baka Na Hausa. Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, Saidu, Muhammad (2014) *Diwanin Waqoqin Baka.* Juzu'i Na Biyu: Century Research and Publishing Limited Kano-Nigeria.

Muhammad, X. (1978). "Waqa Bahaushiya". cikin *Studies in Hausa Language, Literature And Culture*. Kano: Bayero University.

Mujaheed, A. (2018). "Hankaka Mai Da Xan Wani Naka: Waqoqin Salisu Sa'in Makafin Zazzau a Bakin Mawaqan Qarni na 21". *Kadaura: Journal of Hausa Multi-Disciplinary Studies,* Vol. 1, No. 4, Special Edition. Department of Nigerian Languages and Linguistics, Kaduna State University-Nigeria.

Mukhtar, I. (2004). *Introduction To Stylistics Theories, Practice And Criticism*. Abuja; Country Side Publishers Vol. I.

Satatima, I.G.(2009). "Waqoqin Baka na Xarsashin Zuciya: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu." Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya (2013) *Makaxi A Mahangar Manazarta:* Jerin Takardun da Aka Gabatar a Taron Qara wa Juna Sani Kan Tubar Muhammadu Gambo Mai Kalangu, Gidan Dabino Publishers.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waqeqeniya". Kundin Digiri na Xaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

**1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

**1.** Yi bayani ma`anar waqar baka.

Waqar baka wani saqo ne cikin zance da azanci da ake rerawa ba faxa kurum ba, ta hikima da fasaha da zavavvun kalmomi waxanda suka dace da saqon, kuma tana zuwa gunduwa-gunduwa da sautin murya da kixa da armashi da gaxa da tafi mai saka zuciya jin daxi. Haka kuma, akwai wasu matakai wato kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma'anar waqar baka, waxannan kalmomi sun haxa da rerawa da hawa da saukar murya da daidaita murya da rauji da naqaltar harshe da hikima da fasaha da kixa da karvi ko amshi.

**2.** Yi bayani kan biyar daga cikin kayan kixan Hausawa tare da misalai.

**Kukuma:** Kukuma kamar goge yake sai dai sautinta ba iri xaya yake da na goge ba.

**Garaya:** Wannan abin kixa ne da ake kaxawa an fi amfani da garaya wajen kixan bori ko na iskoki.

**Kuntigi:** Kuntigi shi ma kaxa shi ake yi amma girmansa bai kai na garaya ba.

**Gurmi:** Gurmi ya xara kuntigi tsawo, shi ma ana kaxa shi ne kamar garaya ko kuntigi.

**Molo:** Molo ya yi kama da kuntigi ko garaya amma ya xara su girma. Shi ma kaxa shi ake yi kuma ana haxa shi da qoqo da duma.

**3.** Mene ne tsarin waqar baka na Hausa ya qunsa?

An bayyana tsarin waqar baka a matsayin awon waqar baka, da irin yadda ya shafi yadda makaxi yake shirya waqa a cikin zubin xiya da dabarun karin murya. Haka nan kuma an qara da cewa, a wannan vangaren, ana duba zubin layuka da yawan xiyan waqa da tsarin rerawa da karin murya da amsa-amon kari da sauran abubuwan da suka shafi awon baka. Xiyan waqa kuwa tamkar rassa ce ta itaciya wadda ake fara hawowa daga gindi kuma a sauka ta qasa. A kowane xa za a sami hawa da sauka.

## Kashi Na 3: Bayani Game da Zube na Baka

**Abubuwan da ke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Tatsuniya
3.4 Labaran Tarihihi ko Tarihi
3.4.1 Labaran Qissa
3.4.1 Hikaya
Auna Fahimta na 1
3.5 Taqaitawa
3.6 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

Idan ana maganar zube na baka, akwaiabubuwa da mai karatu ya kamata ya lura da su, daga ciki akwai ma`ana da tarihin samuwar wannan zube da kuma rabe-rabensa. Adabin baka adabi ne da ya samu tun kafin Bahaushe ya fara hulxada baqi, akwai hanyoyi da dama da Bahaushe yake amfani da su domin ilimantar da kuma tarbiyantar da `ya`yansa ta yadda za su tashi cike da dabaru da kuma ilmin zamantakewa. Daga cikin waxannan hanyoyi, akwai labarai da ya tanadar waxanda ake kira zube na baka, sun kuwa haxa da maganganunsa na azanci da labarai ko tatsuniya da tarihi ko tarihihi.

Wannan kashi bayani ne kan zube na baka, wato zuben da ake qagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka, musamman abin da ya shafi dogayen labarun baka da suka haxa da tatsuniya da hikaya da qissa da kuma tarihi da tarihihi.

### 3.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a fahinci yadda zube na baka na Hausa yake da yadda za a iya gane shi, ana sa rai xalibai za su fahimci :

- Ma`anar zube na baka da yadda za iya gane shi.
- Ire-iren zube na baka
- Bambancin zube na baka da sauran sassan adabin baka.

### 3.3 Tatsuniya

Babu wani mahaluki wanda zai ce ga lokacin da aka fara tatsuniya, masanan na ganin kwatankwacin daxewar tatsuniya kwatankwacin kafuwa al`umma. Bahaushe bai kevanta da sauran al`ummomi ba wajen

tanadarwa kansa hanyoyi da za su ilmantar da faxakar da kuma nishaxantar da al`umma. Tatsuniya tana daga cikin manyan rasa na adabin bakan Bahaushe vangaren zube, kuma qagaggen labari ne da Bahaushe kan ba `ya`yansa domin su tashi cikakku kuma kamillu. Gusau, (2006) cewa ya yi "tatsuniya wani tsararren labari ne wanda magabata (musamman tsofaffin mata) suke shiryawa cikin hikima da nuna qwarewa da naqaltar harshe da ya qunshi wata shiryarwa da nuni zuwa ga halaye da ilmin zaman duniya, sannan da saka nishaxi da raha ga rayuwa da kuma cinye dare". Hausawa suna da labaransu na tatsuniyoyi waxanda su ne suka qirqiro su da kansu don nishaxi da koyarwa. Sun mallaki wannan hanya ta bayyana matsayinsu, musamman ga yara, tun jimawa, ba sai da suka cuxanya da wata al`umma ta koya masu ba. Hasali ma dai ba za a iya bugun gaba a ce ga lokacin da aka fara yin ta ba. Tatsuniya gadon gado ce, ta ginu a sakamakon tasirin al`adar rayuwa ta Hausawa, har ta zama ruwan dare game duniya (Yahya da wasu 1992). Haka kuma, labari ne qagagge ake harhaxawa a tayar da gangar jikin tatsuniya, har a kaxa ta, ta bayar da wani amo da ake son sadarwa ga masu saurare.

Masana da manazarta sun ayyana tatsuniya a matsayin makaranta ta Bahaushe, ta nan yakan ilimantar da `ya`yansa dabarun zaman duniya tun kafin Bahaushe ya sadu da baqi. Al`adun Hausawa ne suka haifar da tatsuniya kuma wajibi ne a yi la`akari da cewa tatsuniya ta samu tun kafin Bahaushe ya iya karatu da rubutu balle ya kafa makaranta. Tatsuniya ta wanzu cikin al`ummar Hausawa wadda tunaninta da hikimominta da fannonin ilminta duk da baki ne akan baza su, daga wannan mutum zuwa wancan da kuma wannan zamani zuwa wancan. Koyo da koyarwa, xabi`ar xan adam ce, saboda haka ya zama tilas ga Bahaushe ya qirqiro wata hanya ta aikawa da hikimominsa da al`adunsa daga zamani zuwa zamani. Xaya daga cikin waxannan hanyoyi ita ce tatsuniya. Ta amfani da tatsuniya Bahaushe kan kaifafa tunanin `ya`yansa.

### 3.4 Labaran Tarihihi ko Tarihi

Waxannan kalmomi guda biyu kusan suna da dangantaka da juna. Tarihi shi ne ruwaito abubuwan da suka faru waxanda suka shuxe, Shi kuwa tarihihi an samo ta ne daga kalmar tarihi ta hanyar liqa wa kalmar xafa-qeya na 'hi', sai ta koma 'tarihihi'. Sai dai abin kula a nan shi ne tarihi dai yana nufin wani labari ne na haqiqa da ya tava faruwa a cikin al'umma. To, amma shi tarihihi za a iya cewa, wani labari ne na wasu abubuwa da suka tava wakana na haqiqa a cikin al'umma, sai dai irin wannan labarin yana cakuxe da wasu abubuwan da ba a tabbatar da faruwarsu ba. Don haka idan aka ce tarihihi, a taqaice ana nufin gurvataccen tarihi, wanda aka cakuxa shi, a tsakanin abin day a faru na haqiqa da wanda bai faru ba. Ana qirqirar Tarihihi a matsayin labari a ka, kuma a adana shi a ka, akan sami sauye-sauye saboda tsawon zamani wajen wanzar das hi daga al`umma zuwa ga wata al`ummar. Wannan dali ne ya sa mutane ke ganin baa bin mamaki ba ne don an sami qarya a cikin tarihihi.Tarihihi, ya qunshi labarai ne na kunne ya girmi kaka, waxanda ba a iya tabbatar da haqiqanin aukuwarsu ba. Kuma labarai ne da suka qunshi abubuwan da

suka danganci rayuwar Hausawa, musamman a jiya, akwai tarihihi kala-kala a qasar Hausa sai dai waxanda suka yi tashe sun haxa da na taririhin Bayajidda da tarihihin sarkin Katsina Korau da tarihihin Wali Xanmarina da Wali Xan Masani ko wani vangaren tarihin Usman Xanfodiyo ko Xanwaire da makamantan su.

Duk wanda ya duba xaya daga misalin da aka bayar zai fahimci labarai ne masu qunshe da gaskiya da qarya duk a cikinsu,wato wani vangare nalabarin qarya ce wani kuma akwai alamun gaskiya.

**3.4.1 Labaran Qissa**

Wani daga cikin misali na zube na baka shi ne Qissa, qissa kalma ce da aka samo daga harshen Larabci wadda ta shige tsundum a cikin adabin Hausa. Ita dai wannan kalma tana xauke da ma'anoni biyu ne a cikin harshen Larabci. Wato ma'ana ta lugga da kuma ma`ana ta zahiri, a luggance, qissa na nufin bibiya ko qididdigewa. Watau mutum ya bi diddigin wani abu har ya zuwa qarshensa, wannan ke nan. A ma'ana ta zahiri kuwa, kalmar qissa na nufin bada labarai dangane da mutanen da suka shuxe, ko kuma bada labarai a kan waxansu abubuwa da suka auku a da. Ko kuma wani labari da ke kara zube da ya qunshi shiryarwa zuwa ga addini ko gaskiya ko neman tsira kan wani abu. A ra'ayin masana da dama sun yi nuni da cewa an fi danganta ma'ana da manufar qissa a kan labarun da suka danganci addini kawai. Watau bayanai a kan rayuwar annabawa da sahabbai da waliyyai da sauran su. Duk da haka akwai wasu labarai na qayatarwa da jawo hankali da za a iya kiran su da qissa, kamar irin qissoshin da suka shafi soyayya. Don haka akan ce qissa wata hanya ce ta cusa wata manufa cikin zukatan masu saurare.

Qissa ta shafi abin da ya bibiyo labarin annabawa kamar yadda ya zo cikin Alqur'ani mai girma, inda ake da surori da suka bayyana labaran annabawa da aka zayyana a cikin Al'qur'ani. Sai dai ita qissar da Bahaushe ke bayani ta shafi wadda aka gina ne bisa tunanin Bahaushe, wato ga yadda labarin yake a zahiri amma a qara masa wani abu ko dai don daxin labarin ko kuma domin a qara qayatar da mai sauraro. Alal misali qissar Annabi Yusuf ko ta Annabi Sulaiman ko kuma ta Annabi Nuhu za a same su da xan bambanci da wadda qur'ani ya zo da ita. Shi ya sa masana suka raba qissar zuwa gida biyu:

**i) Qissar Cinye Dare:** Wadda ta qunshi labarai da zantuttukan da mutane suke yi don cinye dare.

**ii) Qissar Addini:** Wannan ta qunshi labarai ne da ake tsarawa a kan wani abu da ya auku na addini a lokacin annabawa da sahabbai da waliyyai da shaihunnai da sauran su.

Qissa labari ne na gaskiya da aka bayar ko ake bayarwa a kan rayuwar annabawa da sahabbai ko waliyyai ko shaihunnan malamai, ko wasu bayin Allah da sauran su da suka danganci addinin Musulunci, musamman waxanda Alqur'ani da Hadisai suka kawo bayaninsu. Shi kuwa Bahaushe ya sami damar sanin wani labari da ake kira da suna 'qissa' bayan cuxanyarsu da Larabawa, suka kuma samu damar rabauta da addinin Musulunci. Don haka a iya cewa tasirin addinin Musulunci da

karance-karancen da suka danganci tafsiri da hadisai da wa’azi wajen watsa addinin Musulunci, su ne suka taimaka wajen samuwar qissa a al’ummar Hausawa.
Akwai Shaihin malami da raba qissa zuwa sassa daban-daban. Daga cikin su akwai Sa’idu Muhammad Gusau wanda ya kasa qissa zuwa nau’i huxu kamar haka:

- Qissar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haqiqa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saqon Ubangiji (Allah).
- Qissar Sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke qunshe da bayanin rayuwarsu.
- Qissar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miqa wuyansu ga addinin Allah.
- Qissar kangararru, waxanda suka bijire wa addinin Allah.

### 3.4.2 Hikaya

Ma`anar hikaya a bayyane take, hikaya labari ne da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma qwari. Wani lokaci kuma takan xauki yanayin qago wasu labaran don qarin bayani kan wani abu ko kwaikwayon sa. Hikaya labari na manyan mutane, ba annabawa ba, da abin da ya faru gare su. Misali, hikayar wani halifa ko sahabi ko wani babban sarki.
Hikaya kuma, takan qunshi wani abin mamaki da ya auku ko kuma dai wani labari mai koya darasi gaz aman duniya (ko ma amfanin lahira). Hikaya kuma tana iya zama ta wani attajiri ko kuma dai wani labari mai koya zaman duniya dangane da yadda mutum zai iya bakinsa, misali, Hikayar Kunkuru Da Gauraki,
Wata’ rana, wasu gauraki guda biyu, za su yi balaguro sai wani kunkuru abokinsu ya roqe su, su tafi da shi. Suka ce masa shi da ba shi da fuffuke ta yaya za su yi tafiya tare ? Amma sai ya nace sai ya sun tafi da shi. Shi kenan, sai suka yi dabara, suka xauko wata sanda kowace tsuntsuwa (gauraki) ta kama gefen sandar guda, shi kuma kunkuru ya riqe sandar da bakinsa, suka tashi da shi. Suna cikin tafiya a sama sai suka ga wani abin dariya na aukuwa a wani gari da suka zo wucewa. Sai xaya daga cikin gaurakin ta ce ; “La, kin ga wani abin dariya, zomo na korar akuya.” Ko da ‘yar’uwarta ta duba ta ga haka sai ta qyalqyale da dariya. Da kunkuru ya ji suna dariya, sai ya buxe baki wai zai tambaye su abin da ya sa suke dariya. Buxe bakinsa ke da wuya, sai ya sullo, ya faxo qasa ya farfashe. (Wai shi ya sa ake ganin bayan kunkuru duk a tsattsage). Wannan hikaya tana koya wa mutum ya iya bakinsa, domin kuwa da kunkuru ya iya bakinsa da haka ba ta faru da shi ba, Xangambo, 2008.

**Auna Fahimta**

| |
|---|
| 1. Me aka fahinta da zube na baka?<br>2. Kawo ire-iren qissa guda uku (3).<br>3. Me ake nufi da hikaya ? |

## 3.5 Taqaitawa

Kamar yadda bayani ya gabata, ana wanzar da zube na baka da fatar baki, ana qirqirar shi ko qaga shi da ka, a kuma adana shi a ka kamar sauran nau'o'in adabin baka. Darasin yabayyana yadda tatsuniya da Qissa da Hikaya suka kasance nau`o`in zube masu dogayen labaru, haka kuma, wasu gajerun zantukan hikima ne don fasalta rayuwa da koya darussa mabambanta, da kuma nishaxantarwa.

## 3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Tatsuniya: Qagaggen labarin baka da magabata suke yi wa yara don su koyar da su wasu darussan zaman duniya.
- Nisaxantarwa: Jin daxi ko farin ciki
- Hikaya: Labari mai ban mamaki da ya abku mai koya darasin zaman rayuwa.
- Rauhanai: Musulman aljannu

## 3.7 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

Gusau, S.M. (2006). Tatsuniya (Gatana): Sigoginta da Hikimominta. Cikin *Mujallar Algaita*, 4,1.

## 3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**1.** Me aka fahinta da zube na baka?

Zube na baka, wato zuben da ake qagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka, musamman abin da ya shafi dogayen labarun baka da suka haxa da tatsuniya da hikaya da qissa da kuma tarihi da tarihihi.

2. Kawo ire-iren qissa guda uku (3)

- Qissar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haqiqa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saqon Ubangiji (Allah).
- Qissar Sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke qunshe da bayanin rayuwarsu.
- Qissar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miqa wuyansu ga addinin Allah.

3. Me ake nufi da hikaya?

Hikaya labari ne da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma qwari. Wani lokaci kuma takan xauki yanayin qago wasu labaran don qarin bayani kan wani abu ko kwaikwayon sa. Hikaya labari na manyan mutane, ba annabawa ba, da abin da ya faru gare su. Misali, hikayar wani halifa ko sahabi ko wani babban sarki

## Kashi Na 4: Bayani Game da Wasan Kwaikwayo na Baka

**Abubuwan da ke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Tashe a Qasar Hausa
4.3.1 Ta Yaya Za a Rarraba Tashe?
4.3.2 Siffofin Kwaikwayo A Sana`ar `Yankama
4.4 Yadda Wasan Gauta Yake a Al`ummar Hausawa
4.4.1 Lokaci da Yadda Ake Aiwatar da Wasannin
4.4.2 Tasirin Wasan
Auna Fahimta na 1
4.5 Taqaitawa
4.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

A cikin adabin baka, akwai wasanni waxanda suke xauke da siffar kwaikwayo, su waxannan wasannin suna da siffofi na sauya kama da sauya murya ko tufafi ko faxi-faxi tsakanin `yan wasa su ne ma`aunan da aka yi amfani da su wajen kira su da wasannin kwaikwayo na baka. Wasu daga ciki suna buqatar motsi da gavuvvan jiki sa`annan wasu daga cikin nau`in adabin baka su biyo baya, irin waxannan sun haxa da tashe da `yan kamanci.

### 4.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a iya tatance wasannin da suke da siffar kwaikwayo a cikin wasannin gargajiya na Bahaushe. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai su fahimci:

- Ma`ana da ire-iren wasannin tashe
- Ma`ana da yadda `yan kama suke da matsayinsu a al`ummar Hausawa.
- Yadda ake aiwatar da wasan gauta da kuma irin fai`dojin dake da ke tattare da waxannan wasanni.

### 4.3 Tashe a Qasar Hausa

Sai da aka sami shigowar musulunci kana wasu wasannin suka bayyana, daga cikinsu akwai wasan tashe, masana sun bayyana ma`anar tashe

kamar haka: Ahmed, (1985:8) ya ce: 'Tashe a kowane bangaren }asar Hausa ana yin shi ne a watan azumi, lokacin watan ya kai kwana goma abubuwa guda uku ne, na farko a tashi jama'a lokacin sahur, kamar yadda kalmar nan "tashe" ta nuna. Dalili na biyu shi ne, don hana mutane wasanni almubazzaranci, na uku ana yin wasannin tashe ne domin nisha]i bayan bu]e baki'. Shi kuma Umar (1980:3) cewa ya yi: 'tashe al'ada ce da aka yi a cikin watan nan mai alfarma wato watan Ramalan. A wannan wata Ubangiji Tabaraka Wata'ala ya umarci Musulmi da yin azumi, ya kuma kwa]aitar da su ga yawaita ayyukan Ibada.

**i. Vullar Tashe A Qasar Hausa**

Duk da yake musulunci ya daxe da shigowa al`ummar Hauusawa, duk da haka babu wani takamaimai lokaci da aka fara tashe, duk da haka, Musulunci ya zo da azumi a matsayin shika-shikansa, a saboda haka ne Bahaushe ya }ir}iri tashin mutane domin yin Sahur. Ana kyautata zaton daga wannan ]abi'a ta tashin mutane domin su yi sahur saboda muhimmancin yin haka daga Alku'ani da hadisan Annabi (SAW) suka fa]i kamar haka: "yin sahur ba wajibi ba ne, amma dai sunna ce mai }arfi domin Manzon Allah (SAW) ya ce, bambancin azuminmu da na Yahudawa da na Nasara shi ne yin sahur wato abinci, ruwa ko dabino mutum ya samu ya ci" Muslim ya ruwaito. Akwai rahama ga wanda ya yi sahur ko da }alilan ruwa ne. Yin sahur na samun sau}in azumi, shi ya sa aka ri}a samun mutane wa]anda suka azawa kansu wannan nauyin aiwatar da wannan aiki ba tare da biyansu wata lada ba. Haka kuma ana ganin kalmar tashe wadda aka sani a yanzu ta samo asali ne daga wancan kalmar ta 'tashi', tashin jama'a da ake yi domin yin sahur. Wai daga nan ne aka sami vullar kalmar tashe.

**4.3.1 Ta Yaya Za a Rarraba Tashe?**

Mutane ne ke aiwatar da tashe, tun da abin haka yake ashe za aiya amfani da masu aiwatarwa a rarraba tashe. Akwai tashe na yara maza, da kuma na 'yan mata, sa`annan akwai tashen Samari matasa.

**-Tashen yara maza, sun ha]a da:** Sakanni-in [iba, ka-yi -rawa, [andu {ununu, Tsoho da gemu, Danda dokin kara, zan buga, kar-ka buga tashi wali da sauransu.

**- Tashen yan mata sun ha]a da:** Samodara, Maryama da Daudu, Asha ruwa, Mai ciki, Auren-gidan- ba-sharu-ba da]I da sauransu.

**- Tashen Samari:** Sun ha]a da Amale mai Jan-kaya, Jatau mai magani, gwauro ya tsinke, kai ni chadi zan tafi, macukule da sauransu.

**a. Matsayin 'Yan Kamanci a Adabin Baka**

Kafin a tsunduma ga bayyana matsayin su, yana da kyau a bayar da ma`anarsu da yadda suke gudanar da harkokinsu a matsayinsu na `yan kama. `Yankama maroqa ne da suka shahara wajen ban dariya dasa mutane nishaxi, `Yan kama masu wasannin ne na Hausa waxanda suka yi kama da `yan gambara ko kuma Na-Uwale ko Xanbashirwa. Da yawa daga cikinsu kasuwanni suke bi suna wasanninsu ana basu abin masarufi. `Yan kama kan yi shiga suna kixa suna amfani da takobinsu na ice wajen kai suka domin su tsorata mutum ko don a yi dariya.

Matsayinsu a cikin al`umma kuwa basu misaltuwa, sai dai a ce suna da qima da daraja a wajen gudanar da ayyukansu. Xaukakar da suka samu ba ta rasa nasaba da yadda suke nishxantar da al`umma da kuma hannunka-mai-sanda a wasu lokuta kan wasu munanan halaye da wasu ke nunawa. Masu hikim na cewa, idan an bi ta Varawo to a bi ta Ma-bi-sahu, manufa anan itace, duk da alfanun da suke da shi, suna kuma da ila ta musamman domin kuwa suna tilastawa a yimasu kyauta don gudun tozarci.

### 4.3.2 Siffofin Kwaikwayo a Sana`ar `Yankama

Shi dai xankama ya kan sa buje ne, da babban riga. Amma fa rigar yakan kwave ta ne ya yi qunzugu da ita a mararsa, watau ya bar gangar jikinsa a buxe. Wasu kayan 'xankama' kuma su ne takobin ice da tasbahar quliquli da garmar sakaina. Duk batun xankama dai ba ya wuce ta abinci. Duk da yake xankama yakan faye ambaton addini musulunci, lamurar addinin nan yakan sake masu kama ne, ya mayar da ginshiqinsu ya zan abinci. Siffofin kwaikwayon da ke tattare da wasan xankama sun haxa da yadda yake kwaikwayon yaqi da kai bara a sukwane ga abokin gabansa ta hanyar yin amfani da takobin ice. A nan takobin iccen shi ne kwatakwacin takobi na zahiri, haka nan mutumin da ya nufa da wannan takobi shi ne tamkar abokin hamayyarsa a fagen fama. Idan kuma yana son ya kwaikwayi `yan hoto, wato masu **Nakiya-da Garma**', xan kama kan yi amfani da garmarsa ta sakaina yana jefa ta sama yana kamawa. Wani muhimmin abu kuma idan yana son nuna bajinta ba ya karvan sadaka da hannu, sai dai a jefa masa shi kuma ya café da baki tamkar dai wata dabba mara hannu.

- **Misalan Waqoqin Xan Kama**

Xan kama, gwani ne na kwaikwayo. Don haka, yakan kwaikwayi waqoqin makaxa da yawa. Misali, 'yan kama, suna kwaikwayi waqoqin sojoji a yaqin Ojukwu inda sukan ce:

> Kanar xan wake ya gudu,
> Manjo fura ma ta gudu,
> Janar funkaso ya gudu,
> Mun ci fanke, mun ci waina,
> Qaryar tuwo ta qare!

Haka kuma, sun kwaikwayi waqoqin Shata da yawa. Misali, inda suka kwaikwayi waqarsa ta "Mata ku yi aure" suna cewa:

> Don na ce mata su yi koko,
> Masu kunu suka tozarta ni,
> Har Attaura har Linjila,
> Shin ina ayar da ta kankare koko?

A maimakon inda Shata yake cewa:

> Wai don na ce mata su yi aure,
> Kaxo ya tashi ya tozarta ni,
> Har Attaura har Linjila,

Har Alkur'ani babban kundi,
Ina ayar da ta kankare aure?

Haka kuma wani xan kama, wai shi Isa Rogo, ya buxe wata tashar rediyo, wai ita Rediyo Mai Jini, inda yake kwaikwayon yadda ake ba da labarai a rediyo, Xangambo, (2008).

Ga labarin yadda wani xan kama ya yi limanci:

- **Limancin Xan Kama**

Wai wata rana, wasu 'yan kama guda biyu, suka ziyarci wani gari, suka je fadar Sarki, aka yi musu iso. Da sarki ya gan su, sai ya yi zaton wasu manyan baqin malamai ne. Da azahar ta yi,aka je masallaci don yin salla. Limamin garin, ya ga yadda sarki ya karvi baqin. Don haka, sai ya ce da xaya daga cikin 'yan kaman nan, "Malam, bisimilla. Ai, sai a yi mana salla." kuma don yana tsoron kada malaman su ci gyaransa a gaban sarki, shi ya sa ya yi haka. Xan kama ya wuce gaba yin salla.'Aka yi salla har sai da aka je sujada ta qarshe, sai xan kama ya qi tasowa. Mutane suka qosa. Zuwa can sai xan kama ya fara mutsu-mutsu, goshinsa na kafe a qasa. Sai ya fara cewa, "Ku sake ni! Wayyo ku sake ni! Ihu! Sun riqe mini goslii!" Ko da jama'a suka ji haka, sai kowa ya tashi a tsorace, ridididi, in ba ka yi, ban wuri, tun daga Sarkin har limamin garin. Da 'yan kama suka ga an tsorata, sai suka zaro gangarsu, suna kaxawa. Haushi ya kama mutane. Suka gargaxe su cewa, bai kamata a kawo shaqiyanci a masallaci ba.

Haka kuma, aka ce, wata rana, wani xan kama ya ziyarci wani ofis na wani babban ma'aikaci. Da ya je, ya sami wani masinja a qofar. Da masinjan ya gan shi, sai ya yi zato shi ma ya zo yin mitin xin da ake yi ne a cikin ofis. Don haka, sai ya miqe tsaye, ya gaishe shi, ya buxe masa qofa. Xan kama ya shiga. Ya sami mutane zazzaune kewaye da tebur da fayiloli. Ko da suka gan shi, sai suka rasa abin da ya kawo shi, domin ba su san shi ba. shi kuma ga shi cikin kaya masu kwarjini da muqami. Don haka, sai wannan ya kalli wannan, wancan ya kalli wancan. Zuwa can dai, sai xan kaman ya ce, "Shin wane ne babbanku?" Ya zazzaro idanu. Da ya ga sun tsorata, sai ya yi wuf ya zaro takobinsa na akwasa, ya sake cewa, "Na ce wane ne babbanku?" Sai ya ga duk suna kallon shugaban, wato Cayaman. Sai ko ya doshi wurinsa da takobinsa a zare, yana zazzare idanu. Da suka ga haka, duk sai suka tashi a guje ridididi, a tsorace. Da ya ga haka,sai ya zaro gangarsa ya buga. Da suka gane xan kama ne, sai suka dawo cikin fushi, amma kuma abin ban-dariya, suka gargaxe shi ya daina irin wannan, Xangambo, (2008).

## 4.4 Yadda Wasan Gauta Yake a Al`ummar Hausawa

*Wasan Gauta* wasan kwaikwayo ne wanda ake yi a fada da kuma wanda talakawa ke shiryawa su gudanar a dandali na musamman, asali abin da aka sani da suna **Drama**da Ingilishi ana kiransa '**Gauta**' ne, Yahaya da Suwaid, (1978).Wasan Gauta iri biyu ne, da wanda ake yi fada da kuma wanda talakawa ke yi a cikin gari. Wanda ake yi a fada, {wara}waran sarki ke yin wasan. Sukan aika a kar~o masu suturu da kayayyakin ado na hakiman da za su kwaikwaya. Kowace baiwa takan nazarci shiga da

halayyar hakimin da za ta kwaikwaya tun kafin lokacin wasan, kuma a lokacin gudanar da wasan ne su hakimai da iyalansu kan kasance 'yan kallo masu ganin hoton yadda suke gudanar da mulki da harkokin jama'a. Suna lura da yadda ake kwatanta halayyarsu da ]abi'unsu da yadda suke tunkarar abubuwan da suka shafi al'umma. Ta wannan hanya ce suke fahimtar wuraren da suke da gyara kuma su gyara da wuraren da suke bu}atar }ara himma don kare lafiyar al'umma da dukiyoyinsu.
Idan aka dubi wasannin da yadda ake gudanar da su sai a ga cewa suna nuna yadda Bahaushe yake yi wa kansa hisabi game da abubuwan da suka shafi mulki. Ta hanyar wasannin ne ake gane abubuwan da aka aikata. Idan masu kyau ne a }ara himma, idan kuwa munana ne, a nemi hanyar kaucewar aukuwar irinsu. Ana }ara himma wajen aikata abubuwan da za su taimaka wajen tabbatar da adalci da tsaro da kyautata zamantakewa tsakanin al'umma. Mahukunta na yun}urin sauke nauyin da Allah ya ]ora masu ta hanyar bayar da ha}}o}in da suka rataya a kansu. Suna kasance wa masu yayyafi da rangwame da lullu~e al'ummarsu da abubuwan alheri. Suna basu kariya da }arfafa tsaron }asa da bun}asa tattalin arzi}i da cinikayya ta sanadiyyar wa]annan wasannin.
[aya ~angare na Wasan Gauta shi ne wanda samari da 'yan mata ke aiwatarwa a Dandali. 'Yan wasan kan kwaikwayi halaye da ]abi'un mahukunta ko da kuwa mahukuntar nan na }ungiyoyi ne ko na al'umma. Akan bayyana wasu munanan halaye da ]abi'u wa]anda suke neman kunno wa cikin al'umma, ana nuna yadda suke da illarsu ta hanyar wasa. Haka ma ta hanyar kwaikwayo akan nuna wasu halaye da ]abi'un mutane marasa kyau, ko wani aikin ashsha ko sakaci ko raggwanci da wani ya yi domin masu aikata wannan aikin su gani su daina. Ya kuma zame wa sauran al'umma hannunka-mai-sanda. Wasannin kan }arfafa aikin gayya da jaruntaka da girmamawa da tausayin marasa }arfi da dogaro da kai. Mutane daga ko ina kan halarci wurin domin kallon wannan wasa, hatta ba}i ma daga {auyuka ma}wabta kan yi tafiya takakka domin halartar wasan.

### 4.4.1 Lokacin da Yadda Ake Aiwatar da Wasannin

Akwai lokuta na musamman waxanda ake aiwatar da waxannan wasannin. Sau da yawa da kaka ne aka fi aiwatar da wasan gauta idan an gama girbe amfanin gona, irin wannan wasa shi wasu ke kira Kalankuwa. Wasu lokutan da ake aiwatar da wasannin sun dogara ne ga irin was an, manufa idan na fada ne za iya aiatar das hi a kowane lokaci.

### 4.4.2 Tasirin Wasan

Kamar yadda sauran wasannin Hausa suke da tasiri, haka ma wannan wasan Gauta ya samu ci gaba a zamanin mulkin mallalka inda aka sami Wasan Gwamna da Wasan Misisi

***Wasan Gwamna*** ya samu ne sakamakon kallon wasan gauta da mahukunta suka rin}a yi a zamanin mulkin mallaka. Turawa masu mulki sun fahinci kyawawan tsarin siyasa da shugabancin Bahaushe, wannan ne yahaifar da Mulki a Kaikaice da aka yi wa Arewa. Ta kallon wannan wasa ne kuma suka fahinci cewa mahukunta za su iya }ididdige yadda suke

aiwatar da mulki tare da fahimtar wuraren da ke bu}atar gyara. A manyan Biranen da Di o ko N.A ko Razdan suke zaune ake aiwatar da wannan wasan. Samari da ‘yan mata ne ke gudanar da wannan wasan ta hanyar kwaikwayar wa]annan mu}amai. Sukan yi shiga irin ta wa]annan shugabanni, ana kwakwayar yadda suke da yadda suke gudanar da sha’anin mulki, Galibi a gaban wa]annan shugabanni da mahukuntan }asa da manyan ma’aikatan gwamnati ake aiwatar da wasan. Akan kuma taru a aiwatar da wasan don jama’a su yi kallo. Abin lura a nan shi ne, duk da cewa mahukunta na zaune don kallon wasannin, masu shirya wasan ba sa samun wani tarna}i wajen tsare-tsarensu da abubuwan da suke son su kwakwaya na daga cikin halayen mahukunta. Inda ake samun tarna}i shi ne ba kowa da kowa ne zai kasance ]an kallo ba a wasannin da ake gudanarwa a fada. Haka kuma, wannan zai gwada wa mutane cewa wasannin kwaikwayon Hausa ha}i}a madubin shugabancin al’umma ne. Wani wasan ma mai kama da ***Wasan Gwamna*** shi ne ***Wasan Misisi.*** Wasu na kiran *Wasan gwamna* da *Wasan Misisi*. A wasan ba Gwamna da mu}arrabansa ne ka]ai ake kwaikwaya ba, maimakon haka ana kwaikwayon matan mahukuntan ne. Suturunsu na sikek da ‘yar rigar wadda Bahaushe yake kira Misisi su ne suturun da ‘yan wasan suke amfani da su wajen aiwatar da wannan wasa. Babu mamaki ma daga nan ne wasan ya samo sunansa. A lokacin wannan wasa akan samu sauya kama ta tufafi da wuri da ‘yan kallo da fa]i-in-fa]i tsakanin masu gudanar da wasan. Wannan ya nuna irin fasahar da Bahaushe yake da ita wajen saurin sauya wa da abubuwansa domin su dace da lokaci.

**Auna Fahimta**

1. Yi sharhi managarci kan aqalla xaya daga cikin wasanni da suka samu sanadiyyar Musulunci.
2. Yi tsokaci mai gamsarwa a kan wasan Misisi.
3. Wasan Gauta iri nawa ne?

## 4.5 Taqaitawa

A taqaice, wannan darasi ya duba wasu wasannin kwaikwayo na baka musamman wasannnin tashe da wasan `Yan kama da kuma wasan Gauta a matsayi misalai na wasannin kwaikwayo na gargajiya. An ayyana su a matsayin wasannin kwaikwayo na baka saboda kasancewar su akwai siffofin wasan kwaikwayo waxanda suka yi katutu a yayin da ake gudanar da su.

## 4.6 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Kwaikwayo: Koyi da abin da wani ya yi.
- Kalankuwa: Wasan da samari da ‘yan mata suke lokacin rani ana kwaikwayon mulki
- Turawa: Mutumin qasar Turai

- ‘Yankama: Mutane masu kixa da waqa haxe da wasu abubuwa na ban dariya.

## 4.7 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari


Ahmed, U.B (1985) *Nau’o’in wasannin kwaikwayon Hausa*. Cibiyar Nazarin Al’adun Nijeriya. Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Muhammad, S. da Yahaya, I.Y (1978) *Darussa Akan Adabin Hausa.* Zaria. Institute of Education, Ahmadu Bello University.

Ibrahim, M.S (1982) “Dangantakar Al’ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa ta Gargijiya”. Kano. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya Jami’ar Bayero.


## 4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Yi sharhi managarci kan aqalla xaya daga cikin wasanni da suka samu sanadiyyar Musulunci.

Duk da yake Musulunci ya daxe da shigowa al`ummar Hauusawa, duk da haka babu wani takamaimai lokaci da aka fara tashe, duk da haka, Musulunci ya zo da azumi a matsayin shika-shikansa, a saboda haka ne Bahaushe ya }ir}iri tashin mutane domin yin Sahur. Ana kyautata zaton daga wannan ]abi’a ta tashin mutane domin su yi sahur saboda muhimmancin yin haka daga Alku’ani da hadisan Annabi (SAW) suka fa]i kamar haka: “yin sahur ba wajibi ba ne, amma dai sunna ce mai }arfi domin Manzon Allah (SAW) ya ce, bambancin azuminmu da na Yahudawa da na Nasara shi ne yin sahur wato abinci, ruwa ko dabino mutum ya samu ya ci” Muslim ya ruwaito. Akwai rahama ga wanda ya yi sahur ko da }alilan ruwa ne. Yin sahur na samun sau}in azumi, shi ya sa aka ri}a samun mutane wa]anda suka aza wa kansu wannan nauyin aiwatar da wannan aiki ba tare da biyan su wata lada ba. Haka kuma, ana ganin kalmar tashe wadda aka sani a yanzu ta samo asali ne daga wancan kalmar ta ‘tashi’, tashin jama’a da ake yi domin yin sahur. Wai daga nan ne aka sami vullar kalmar tashe.

2. Yi tsokaci mai gamsarwa a kan Wasan Misisi.

A wasan Misisi ba Gwamna da mu}arrabansa ne ka]ai ake kwaikwaya ba, maimakon haka ana kwaikwayon matan mahukuntan ne. Suturunsu na sikek da ‘yar rigar wadda Bahaushe yake kira Misisi su ne suturun da ‘yan wasan suke amfani da su wajen aiwatar da wannan wasa. Babu mamaki ma daga nan ne wasan ya samo sunansa. A lokacin wannan wasa akan samu sauya kama ta tufafi da wuri da ‘yan kallo da fa]i-in-fa]i tsakanin masu gudanar da wasan. Wannan ya nuna irin fasahar da Bahaushe yake da ita wajen saurin sauya wa da abubuwansa domin su dace da lokaci.

3. Wasan gauta iri nawa ne?

Wasan Gauta iri biyu ne, da wanda ake yi fada da kuma wanda talakawa ke yi a cikin gari. Wanda ake yi a fada, {wara}waran sarki ke yin wasan. Sukan aika a kar~o masu suturu da kayayyakin ado na hakiman da za su kwaikwaya. Kowace baiwa takan nazarci shiga da halayyar hakimin da za ta kwaikwaya tun kafin lokacin wasan, kuma a lokacin gudanar da wasan ne su hakimai da iyalansu kan kasance ‘yan kallo masu ganin hoton yadda suke gudanar da mulki da harkokin jama’a. Suna lura da yadda ake kwatanta halayyarsu da ]abi’unsu da yadda suke tunkarar abubuwan da suka shafi al’umma. Ta wannan hanya ce suke fahimtar wuraren da suke da gyara kuma su gyara da wuraren da suke bu}atar }ara himma don kare lafiyar al’umma da dukiyoyinsu.

## RUKUNI NA 2: YADDA AKE GANE ADABIN BAKAN BAHAUSHE

### Kashi Na 1: Tsari

**Abubuwan da ke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Ma'anar Tsari
1.3.1 Saqo/Jigo
1.3.2 Salo
1.3.3 Zubi
Auna Fahimta na 1
1.4 Taqaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

A nan, an yi bayanin yadda za iya gane adabin baka na Hausawa, kamar mutum ne ya je kasuwa, ana bu}atar ya siyo abu kaza da kaza. Ta yaya zai iya gane wannan abu ba tare da an bayyana masa yadda zai gane wannan abin ba? Idan kana neman ka gane yaya adabin baka yake, to akwai abubuwan da za ka lura dasu wa]anda za su bayyana maka yadda adabin yake. Saboda haka abubuwan da aka yi bayaninsu a nan, suna magana akan kowane yanki na adabin baka walau wa}ar baka ko zube na baka ko wasannin kwaikwayo na baka.



### 1.2 Manufofin Darasi

Babu shakka wannan darasi na da manufofin da ake fatar xalixbai su fahimta. A san ma`anoni tsari da yadda tsarin adabin baka ya sha bamban da rubutaccen adabi da kuma yadda ake amfani da su wajen nazartar ayyukan adabin baka.



### 1.3 Ma'anar Tsari

Tsarin adabin baka ba mai wuyar fahimta ba ne, duk abin da aka ce yana da tsarinsa na musamman to kuwa bas hi da wuyar ganewa. Tsarin adabin baka a nan yana nufin wasu fitattun alamomin da ake iya shaida wani abu, su wa]annan alamomi su ke siffanta abin da ake so a yi magana a kansa. Don haka za a iya shaida adabin baka ne da kuma irin nagartarsa ta hanyar tsarin da ke biye. Wa]annan tsarin sun bambanta daga wannan nau`in adabin baka zuwa ga wani nau`in. Misali idan wasan kwaikwayo na baka ne, ba ya bu}atar tsara `yan wasa da kayayyakin wasa ko wurin da za a

aiwatar da wasan. Haka nan kuma idan wa}ar baka ce, ba ta bu}atar wasu tsare-tsare na baitoci ko amsa amoko }afiya da daimakamantansu. Zube nabaka shi ma yana da nasa tsarin, dole ne sai an sami mai bayar da labari wanda zai iya kasancewa a bayan fage ko kuma a cikin fage, sa`anna kuma a sami masu saurare, su wa]annan tsarin su ne ke tabbatar da nagartar kowane aikin adabin baka, Kuma su ke nuna irin hikima da fasahar da al`umma take da su. Ta hanyar wa]annan tsarin ake gane matsayin adabin baka da irin gudummuwar da ya bayar ga al`umma. Baya ga wa]annan tsarurrukan, ana kuma duba sa}on da adabin yake isar wa ga jama`a da kuma yadda zubi da taurari ko masu isar da aikin adabin suke. Bari mu fara da sa}on da adabin baka yake ]auke da shi.

### 1.3.1 Saqo/Jigo

Sa}o ko jigo shi ne manufar da ake so a cimma a kowane irin abu. Masana da Manazarta suna amfani da wannan kalma ta jigo don bayyana sa}o ko wata manufa ko kuma ma}asudin da ake so a isar ga al'umma. A wa}ar baka, sa}o na nufin turke ko manufar da wa}a ke ]auke da ita ga masu saurare, haka nan a wasan kwaikwayo, sa}o na nufin manufa ko jigon da aka gina wasan a kansa don mutane su himmatu ko su farka. A cikin {amus na ke~a~~un kalmomin adabi, Shipley, (1955:417) ya bayyana ma'anar jigo da cewa: "Shi ne abin da ake magana a kai. Shi ne kuma abin da aka }udurta ko aka aikata. Ko kuma wani sa}on da wani labari ke isarwa."

Haka kuma in an duba {amus na Cuddon, (1977:680) An ce "Magana ta gaskiya, jigon wani rubutu ba yana nufin maganar da rubutun yake yi ba ne illa wata manufa ta musamman wadda aka bayyanata kai tsaye ko a fakaice."

Masana irin su Farfesa Yahaya, (1997:75) ya bayyana ma'anar jigo (wa}a) da cewa, jigo na nufin sa}o ko manufa ko bayani ko ruhin da wa}a ta }unsa wanda kuma shi ne abin da wa}ar ke son isarwa ga mai saurare, ko karatu, ko nazarinta. Ya kamata a lura a nan cewa wannan ma'ana za ta iya ]aukar duk wani fanni na harshe, da adabi, da al'ada.

Farfesa Yahaya, I. Y. da sauransu, (1992:47) an bayyana ma'anar jigo da cewa, shi ne dai "sa}o" ko ginshi}in al'amari da abu yake ]auke da shi. Wasu kuma kan fassara jigo da cewa shi ne "manufar abu" ko "}ashin bayan abu" ko muhimmin darasin da yake ]auke da shi ko yake koyarwa.

Gusau, (2003:28) Ya bayyana ma'anar Turke (jigo) da cewa, shi ne abin da (wa}a) take magana a kansa wanda ya ratsa ta tun daga farkonta har zuwa }arshenta. Wato dai turke shi ne ainihin manufar abu.

Mukhtar, (2004:31) ya ambaci jigo da cewa, shi ne }ashin bayan labari, wato ma}asudin da aka gina labari a kansa.

Dangambo, (1981:5) ya ambaci cewa, abin da ake nufi da jigo shi ne sa}o, manufa, ko abin da (wa}a) ta }unsa, wato abin da take magana a kai.

### 1.3.2 Salo

Salo ma wani ~angare ne da ke ayyana yanayin tsari a adabin baka, ta hanyar da aka bi ko irin salon da aka yi amfani dashi kan tabbatar da yadda

ake iya gane adabin baka. Idan akwai salo na musamman da aka san rubutaccen adabi dashi, ko shakka babu adabin baka yana da nasa salon daya ke~anta da shi. Bari mu ga ma`anar salo daga bakin masana, don samun haske,a wa}a, Abdullahi (2001:3) na cewa: salo na nufin duk wata dabara ko hanya a cikin wa}a wadda aka bi domin isar da sa}o. Ita wannan dabara ko hanya tana yi wa wa}a kwalliya ta yadda sa}on wa}ar zai isa ga mai sauraro ko karatun wa}ar.Ana ganin ba a yi kuskure ba idan aka ce wannan ma'ana ta salo da aka gani nan ita ce dahir a duk inda aka ka]a ko aka raya, kuma ta kowace fuska aka dubi kalmar salo.Wannan ma'ana, ita ta sa masana irin su Dangambo (1981) a cikin Abdullahi (2001:3) suka kawo wasu muhimman tubalan salo guda takwas. Wa]annan tubalan gina salo kuwa su ne:

1- Mallakar kalmomi
2- {irar Jumla
3- Nau'o' in jumla
4- Siffantawa
5- Rauji
6- Tsarin Tunani
7- Jaddadawa
8- Dangantakar tsari

A ~angaren zube kuwa, Mukhtar, (2004:34) na cewa; Abubuwan da akan nazarta a }ar}ashin salo wanda kuma daga kansa ake yanke hukunci a ce salon maibayar da labari ya }ayatar, ya yi armashi, ko kuwa ragon salo ne da shi, sun ha]a har da nazarin irin kalmomin da ya yi amfani da su wajen gina labarinsa, da kuma adon magana, da karin magana da maganganun hikima, da kuma tsarin ginin jimlolinsa. Salo na nufin duk wasu dabarun jawo hankali da mai bayar da labari kan bi wajen }o}arin jawo hankalin mai sauraronsa, gani ko kuma mai karantawa. A nan ana nufin duk wasu dabarun jawo hankalin mutum zuwa ga abin da yake saurare don a cinma fahimtar ainihin sa}on da ake son isarwa. Wannan ne ya haifar da wanzuwar salo iri daban-daban, wa]anda suka ha]a da mi}a}}en salo da salo mai armashi mai karsashi, da raggon salo. Haka kuma salo na iya zama sabo ko tsoho. Abin fahimta a nan shi ne, a zube idan aka ambaci salo, to ana duba harshen da mai bayar da labari ne ya yi amfani da shi wajen isar da sa}onsa.

Idan kuwa ka gangaro ga zantukan hikima ko wasan kwaikwayo, Crow, (1983:55) ya ce: Salo ko harshe na nufin yadda harshen 'yan wasa ta dace da irin mu}amansu da aikace-aikacensu, wato salon da kowanne ]an wasa ko 'yar wasa suka bi wajen sarrafa harshensu a wasan kwaikwayo, wannan kam ya shafi dukkan fannonin wasan kwaikwayo. Idan an ce wane gwarzon wasa ne to akan gane shi ta abubuwan da yake fa]i ko ya aikata da kansa. Wa]annan abubuwa kuwa su ake son aga yadda aka zurfafa amfani da su don cimma manufar wasa. Ya zama wajibi (in har za a yi adalci a nazartar harshen 'yan wasa) a fahimci cewa ba ma'ana ta zahiri a zantuttukan hikima ko na 'yan wasa ita ce ka]ai za a duba ba har ma da sakamakon da maganar ta haifar a mahallin da aka yi ta. Wasan

kwaikwayo harha]uwar wasu aikace-aikace ne don su isar da wata manufa, ashe fa]i-in-fa]in ‘yan wasa dole ya kasance yana da dangantaka da aikace-aikacensu kafin a gane ha}i}anin sa}on da ake son a isar.
Cuddons, (1955:655) na cewa; aiki ko wani motsi shi ma alamtawa ne (wanda ake amfani da shi,tauna le~e na da wata manufa ta mugunta. Haka kuma tafa hannu na da manufar yabawa. [aga hannu kuwa na da manufar girmamawa ce. Duk wa]annan suna cikin abubuwan dubawa kafin a yi sharhi a kan hausar ]an wasa ko ‘yar wasa.

**1.3.3 Zubi**

Kamar yadda ake gane nau`o`in rubutaccen adabi ta hanyar yadda aka tsara adabin, haka nan abin yake ga adabin bakan Hausawa. Zubin labari ko wa}a gagarumin fage ne na nazarin adabin baka, zubin wa}ar baka ya sha bamban da zubin rutattun wa}o}I, haka nana bin yake ga zube ko wasan kwaikwayo. Masanin Abrams, (1981:159) ya ce zubin wasan kwaikwayo na magana ne akan yadda aka tsara wasa ta yadda abubuwa suke gudana, daga wannan mataki zuwa wannan mataki. Wannan ya ha]a har da ayyukan ‘yan wasa tun daga farko har zuwa }arshe domin cimma manufar shirya wasan.
Zubi na nufin yadda aka tsara abubuwa a cikin wasa, ko wa}a ko }ir}irarren labari. Aristotle, (1952:685) ya bayyana sifofin da zubin wasa ya }unsa kamar haka: “Ana bu}atar zubi ya kasance cikakke, wato ya kasance da farko da tsakiya da }arke. Kuma ya kasance yana da ]inki wato ha]uwar aiki da wuri da lokaci inda idan aka gusa ko aka cire ]aya saura na iya rugujewa ko gurguncewa.
Wasa wanda ya amsa sunansa ko yake so ya amsa, dole ne ya kasance yana da ha]uwar wa]annan abubuwa guda uku, wato ha]uwar wuri da lokaci da kuma aiki. Idan ana so wasa ya }ayatar a yi amfani da sananen wurare da ta}aitaccen lokaci kada a nuna cewa wasan ya ]auki wasu kwanaki ko shekaru ana gudanar da shi, ko da kuwa ana so a nuna irin wa]annan kwanaki ko shekarun a iya yin haka ta yin amfani da mai shela ko a sharar fage cikin rubutaccen wasan kwakwayo, amma a wasan kwakwayo na talbijin ana yin haka ne ta nuna cewa (bayan shekara kaza ko kwana kaza, ko makonni) sai kawai wasa ya ci gaba tare da jan hankalin mutane cewa sun yarda tamkar an yi wa]annan shekarun ko kwanakin.
Akan sami wani lokaci zubin labari ya kasance yana ]auke da wani labarin daban a cikin uwar labara, wato ga uwar labara na tafiya tiryan tiryan sai a sami tsarma wani labara na daban a cikin uwar labari. Idan an sami haka to shi ake kira ‘kauci’, Abrams, (1981:161) ya ce: Kauci na nufin a shigar da wani labari ko wata matsala ta daban mai dangantaka ko akasin haka da uwar labari ko wasa, akan yi haka ne don a }ayatar da uwar sa}on da ake so a cimma. Ba ga na abin ya tsaya ba, a wa}a ma akan sami wannan tsarin inda ake tsarma wani abin a cikin ainihin wa}ar da ake yi tun farko. Sau da yawa mai bayar da labiri kan sake waiwaya wa baya ga wani abu day a faru a cikin labarin da yake bayarwa don ya }ara kaifafa fahintar masu saurarensa, haka nan ma a was an kwaikwayo nab aka, akan

waiwaya baya don jaddada wata manufa ko jawo hankalin mai saurare ko karantawa. Abrams, (1981:161) Ya ce: A tsari irin na wasan kwaikwayo akan yi waiwaye don }ayatar da wasa ko jaddada wata manufa wadda ake son jama'a su rin}a tuna ta a kowani lokaci a cikin ayyukan adabi. Masana irin su Shipley (1955:310) Sun bayyana zubin wasan kwaikwayo na dauwama ne bisa sanannen tsari na farkon wasa a inda a wannan lokaci ake fara gina matsalar ko gabatar da }alu-balen da yake cikin wannan wasa, wanda zai sa mai kallo ya za}u da son ganin yadda za a warware wannan matsaralar ko }i}i-}a}a. Akwai tsakiyar wasa ko kuma in ce }ololuwar wasa, a nan ne matsalar wasan kan rinca~e. Wani lokaci rincabewar wasa na aukuwa ne a dai-dai lokacin da aka fara wasa. Wani lokaci kuwa a tsakiyar wasan ne ake samun wannan rinca~ewar. Sai }arshe ko kuma gangara inda ake samun lafawa da sulhu don warware matsalar cikin farin ciki ko kuma cikin ban tausayi.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana wasu daga cikin tsarin adabin baka da ka sani.
2. Me ake nufi da jigo ko manufa a fagen nazarin adabin baka?
3. Bayyana abin da ka fahimta da salo da ire-irensa.



## 1.4 Taqaitawa

Muhimman batutuwan da wannan darasi ya tavo su ne cewa a waqar baka ba a kula da yawan baiti ko xango ko kuma qafiya, idan ma akwaiabin daya fi fice a matsayin tsarin waqar baka shi ne kasancewar akwai `yan amshi, da kixa da rawa da dai sauransu. Shi kuwa wasan kwaikwayon baka ko zube nabaka na buqatar mai bayar da labari ko masu kwaikwayar halayyar jama`a kuma a gaban masu kallo ko saurare. Daga nan darasin ya tavo saqon da adabin yake xauke da shi ko yadda zubin wasa ko labari yakan kasance.Wannan darasi ya duba tsarin da ke bayyana nagartar adabin baka. An fahinci cewa baya ga nishaxi, adabin baka yana taimakawa wajen ilmantarwa da faxakarwa. Haka nan kuma nazartar salo da zubin kowane iri daga cikin nau`o`in adabin baka na bayar da damar a fahinci irin gwanintar harshe da qyale-qyalen jawo hankalin da aka yi a cikin wannan adabin bakan.

## 1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Baiti: Layukan waqa 'yar tagwai ko qwar uku ko huxu ko kuma biyar.
- Qafiya: Sautin haruffan qarshen layukan waqa masu kama iri xaya.
- Kixa: Bugun ganga ko kalangu da abin bugawa.
- 'Yan amshi: Mutane masu taimaka wa mawaqi a yayin gudanar da waqa.



## 1.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Abrams, M.H. (1981): *A Glossary of Literary Terms.* Six Edition Halt Rinehart & Wiston, New York.

Abdullahi, B.Y. (2001): *Salo Asirin Waka* Fisbas Media Kaduna.

Cuddons, J.A (1977). *A Dictionary of Literary Terms*. Revised Edition, London.

Dangambo, A. (1984). *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Triumph, Kano

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka.* Benchmark Publishers Limited, Kano.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin {agaggun Labarai.* Benchmark Publishers Limited, Kano.

Shipley, J.T. (ed) (1955). *Dictionaryof World Literary Terms.*Allens & Unwin Ltd London.

Yahaya, I.Y. (da wasu) (1992). *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare* 1 – 3, Ibadan University Press.

Yahaya, A. B. (1997). *Jigon Nazarin Wa}a* Fisbas Media Service Kaduna.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Bayyana wasu daga cikin tsarin adabin baka da ka sani.

Tsarin adabin baka a nan yana nufin wasu fitattun alamomin da ake iya shaida wani abu, su wa]annan alamomi su ke siffanta abin da ake so a yi magana a kansa. Don haka za a iya shaida adabin baka ne da kuma irin nagartarsa ta hanyar tsarin da ke biye. Wa]annan tsarin sun bambanta daga wannan nau`in adabin baka zuwa ga wani nau`in. Misali idan wasan kwaikwayo na baka ne, ba ya bu}atar tsara `yan wasa da kayayyakin wasa ko wurin da za a aiwatar da wasan. Haka nan kuma idan wa}ar baka ce, ba ta bu}atar wasu tsare-tsare na baitoci ko amsa amoko }afiya da daimakamantansu.

2. Me ake nufi da jigo ko manufa a fagen nazarin adabin baka?

Sa}o ko jigo shi ne manufar da ake so a cimma a kowane irin abu. Masana da Manazarta suna amfani da wannan kalma ta jigo don bayyana sa}o ko wata manufa ko kuma ma}asudin da ake so a isar ga al'umma. A wa}ar baka, sa}o na nufin turke ko manufar da wa}a ke ]auke da ita ga masu saurare, haka nan a wasan kwaikwayo, sa}o na nufin manufa ko jigon da aka gina wasan a kansa don mutane su himmatu ko su farka.

3. Bayyana abin da ka fahimta da salo da ire-irensa.

Salo na nufin duk wasu dabarun jawo hankali da mai bayar da labari kan bi wajen }o}arin jawo hankalin mai sauraronsa, gani ko kuma mai karantawa. A nan ana nufin duk wasu dabarun jawo hankalin mutum zuwa ga abin da yake saurare don a cinma fahimtar ainihin sa}on da ake son isarwa. Wannan ne ya haifar da wanzuwar salo iri daban-daban, wa]anda suka ha]a da mi}a}}en salo da salo mai armashi mai karsashi, da raggon salo. Haka kuma salo na iya zama sabo ko tsoho.

## Kashi Na 2: Yin Amfani da Harshe

**Abubuwan da ke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Yaya Harshe Yake?
2.3.1 Harshe a Matsayin Kafa ta Sadarwa
2.3.2 Harshe a Matsayin Kafa ta Bayyana Tunani
Auna Fahimta na 1
2.4 Taqaitawa
2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa

Maraba da haxuwa da ku xalibai a wannan darasi inda za a nuna ma mai karatun cewa hanya mafi sauri da ake gane adabin baka ita ce ta amfani da harshe. Yin amfani da harshe na daga cikin hanyoyin da xan adam yake bi wajen sadarwa a tsakinsa da mutane. Wannan ya nuna mana cewa,Hausawa ma ba a barsu a baya ba wajen amfani da harshe don sadarwa a tsakanin al`umma, haka kuma suna amfani da harshe don bayyana irin tunaninsu game da rayuwa, hanya ta baje kolin basirar da Allah ya yi masa. A cikin wannan darasi,akwai bayanin yaddaharsheke taimakawa wajen gane adabin baka na Bahaushe da kuma matsayinsa ga al`umma. Ba anan abin ya tsaya ba, za a duba irin gudummuwar da harshe ke bayarwa ga kaifafa tunani da faxin ra`ayi da lallashi da qyale-qyalen jawo hankali ko tunzurawa a inda bukatar haka ta taso

### 2.2 Manufofin Darasi

A qarshen wannan darasi, ana fatar xalibai su iya gane:

a. Yadda Harshe Yake
b. Matsayinsa na kafa ta sadarwa
c. Adabin da duk aka wanzar das hi da harshe, shi ne adabin baka.

### 2.3 Yaya Harshe Yake?

Kamar yadda kowane nau`in adabi yake da nasa harshen haka ma adabin bakan Bahaushe yana da nasa harshen na musanman. Masana sun bayyana wasu abubuwan day a kamata a lura das u yayin da ake bayar da labari ko ake wa}a ko kuma ake wanzar da wani wasa a aikace. Yakasai, (2012) ya ce, a duk lokacin da Bahaushe zai fa]i wani zance, ko yake hira

ko magana ko kuma yake bayar da umurni, to akwai abubuwa guda uku da sukan zo cikin zuciyarsa:

1. Darajar mai saurare a idanunsa, wato a idanun mai bayar da labarin.
2. Abin da ake maganar/hirar/ta]in ko zancen a kansa.
3. Wurin da ake gudanar da hul]o]i/ mu'amaloli.

Idan ]aya daga cikin wa]annan abubuwa uku ya canza, to tilas jigo da kayan cikin labarai su canza.Haka yana faruwa saboda yadda Bahaushe yake fa]a wa na }asansa labarai, ba haka zai fa]a wa abokinsa ba. Lokacin kuma da zai fa]a wa na gaba, tilas ya sauya ba kamar yadda ya fa]a wa abokinsa ba. Bayan haka dai, ha}}in mai bayar da labarai ne ya sami kalmomin da yake ji su ne suka dace a yi amfani da su wajen magana.

Dangane da darajar mai saurare a idanun mai magana kuwa, sau da yawa mutum yakan zo wurin taron jama'a ya tarar suna hira, amma sai ya ji tsoron sa baki. Wannan yana faruwa ne saboda la'akari da auna shekarunsa, wayewar kansa, zurfin ilminsa, darajarsa a idanun masu hirar da kuma tasu darajar a gare shi (cf. Gadanya, 1977). Ga misali' a al'adar Hausawa yaro ba ya sa baki cikin hirar manya sai ko in su manyan ne suka gayyace shi kuma gayyatar takan kasance ta hanyar neman bayani game da wani abu, sa'annan ya sami damar bayani. Duk da haka, lokacin da zai yi magana sai ya yi tunanin irin jama'ar da yake yi wa magana, kana kuma darajarsu a idanunsa ta zo cikin zuciyarsa.

Haka kuma harshen da mai ba da labari ya yi amfani da shi, ta nan ne za a iya sanin yadda ya ]auki wanda yake saurarensa. Wannan tsari ya dace da ra'ayin Wolfram da Fasold (1974) cewa, 'duk taron jama'a da yadda kowa yake magana'. Saboda haka tilas ne yadda ka fa]a wa wannan labarai ba haka za ka fa]a wa wancan ba, domin kowane mutum na da bakin darajarsa ga sauran jama'a.

### 2.3.1 Harshe a Matsayin Kafa ta Sadarwa

Kafar sadarwa bata tsaya ga yin amfani da harshe ka]ai ba ne, akwai hanyoyi wa]anda masana suka zayyana wa]anda za a iya sadarwa ba tare da an furta wata kalma ba. Ire-iren wa]annan hanyoyi sun ha]a da amfani da alamomi ko isharori ko kuma yin amfani da wasu sassan jikin mutum domin isar dasa}o. Idan kuwa muka dawo ga amfani da harshe a matsayin hanya da za iya shaida adabin baka, nan ma bayanan a bayanai suke. Mun dai san cewa ]aya daga cikin hanya da ake wanzar da adabin baka ita ceta amfani da harshe. Wannan shi ya sa ma ake kiran adabin da adabin baka, wato adabin da ake wanzar dashi da baki ta hanyar amfani da harshe. Ta hanyar harshen ne ake gane irin zantuttukan da mai magana ya yi amfani dasu. Ana iya gane nau`in adabin daaka yi ta hanyar nazartar harshe ko hausar da aka yi amfani da ita a cikin adabi. Ta hanyar harshe ake iya shaida nagartar aikin adabi. Shin wannan adabin baka ya tsaru ko kuwa harshen lami gare shi.

Idan kuwa ana batun sadarwa da harshe, to ko shakka babu harshe muhimmiyar kafa ce ta sadarwa cikin zamantakewa. Wato idan aka yi amfani da harshe domin sadarwa, to ko shakka babu za a samu yana ]amfare da al'ada ta hanyoyi daban-daban. Kalmomi da al'umma suke

furtawa, da su ne ake bayyana al'amuran da suka shafi rayuwarsu, wato gaskiya da tunani da kuma harkoki da ake bayyanawa a matsayin tarin ilmi da sauran al'ummu ke fa'idantuwa da su. Hasali ma, kalmomi suna bayyana ]abi'ar duk wanda ya yi amfani da su cikin tadodi. Ta wannan haujin, harshe yana bayyana hanyoyin rayuwa.
Sa`annan kuma, al'ummu ko rukunai na jama'a ba kawai suna bayyana }warewa ba ne, wato suna kuma sarrafa }warewa cikin harshe domin ]orewar zamantakewa. Suna isar da sa}onni ta hanyoyi daban-daban kamar ta amfani da salula ko }ib]au ko wasi}a ko karatun jarida ko kuma hira da ta]i da juna kai tsaye. Hanyoyin da al'umma ke amfani da su (a magance ko a rubuce) suna da ma'ana wajen mu'amala musamman ma idan aka yi la'akari da yadda ake sarrafa hawa da sauka na muryar masu magana da karin lafazi da salon ta]i da kuma ishara.
Haka kuma, harshe tsari ne na alamomi da ke ]amfare da al'ada da }imar masu amfani da shi cikin amfani da harshe. Wato al'umma na kallon harshensu a matsayin alama ta tantance matsayi cikin zamantakewa. Ta wannan }aulin ma, harshe ya zama linzamin al'ada. Sauran maganar ita ce, harshe hanya ce ta bayyana da kuma musayar tunani da batutuwa da labarai domin ya]a ilmi. Tare da dalilai na zamantakewa da tarihin canje-canje domin cigaba, ta wannan haujin, harshe yana matsayin wata kafar sadarwa ta musamman da take ]amfare ga 'yan Adam, kuma wadda ta bambanta da sauran hanyoyin sadarwa kamar na dabbobi ko }ir}irarren harshe. Wato al'amari ne da ya }unshe rayuwar ]an Adam gaba ]ayanta da kuma harshensa kamar Hausa.

### 2.3.2 Harshe a Matsayin Kafa ta Bayyana Tunani

Yin amfani da harshe wajen sadarwa tsakanin mutum da mutum na ]aya daga cikin hanyoyin da suka bambanta ]an adam dadabbobi. Duk da yake su dabbobin ma suna da tasu hanyar ta isar da sa}o a tsakaninsu, amma dai bata amfani da harshe ba. Harshe na taimakawa a fahimci sa}on da mutum yake son isarwa ga ]an uwansa. Da harshe ne ake sanar da duk abin da ake bu}atar a sanar da mutum ko don a da]a]a koya faranta, ko a ~ata ko kuma a tunzurar da zuciyar mai sauraro. Da wannan harshe ne `yan siyasa ke jan hankalin jama'a har su yadda da manufofinsu. Abubuwan da mutum ya tsara a ransa su ne sakamakon tunanin da ke cikin zuciyarsa, babu wata hanya da za a iya gane wannan tunani ko ra`ayi ba tare daya furta ba. Abubuwan da zuciya ta tsara da tunane-tunannen jama`a musamman ayyukan da suka shafi adabi ana furta su tabaka ne. Mawa}i yana furta zantukar wa}arsa ne bayan sun tsaru a zuciyarsa kana sai ya amayar da irin wannan tunani tabaka. Idan kuwa yanayin yadda al`umma ta ]auki rayuwa ce, misali irin tunaninta game da rayuwa, nan ma ana furtawa ta baka. Bari mu ]auki karin maganar Bahaushe guna ]aya a matsyin misali, (]alibai na iya ]aukar duk wani karin maganar da suka fi fahimta a rayuwa su yi amfani da ita don fito da irin tunanin al`umma) "Allah baya ba mai wu}a nama" wannan karin maganar na bayyanawa mutane sau da yawa yana faruwa a rayuwa cewa ga wani mutum na neman abu ido a rufe, amma bashi da hali, wani can kuwa ya sami halin

amma ya }i amfani da wannan damar daya samu wajen cin moriyar ko amfanin da wannan abu ke samarwa. Kamar ]alibi ne mai son karatu amma bashi da ku]i ko mataimakin da zai agaza masa har ya kammala wannan karatu, amma a kusa da shi ga wani ]an gata can gefe guda ana lallashinsa da ya yi karatu amma ya }i yi, in an sami yanayi irin wanna, za iya amfani da Karin Magana na sama don fayyace abin da ake nufin cikin `yan kalmomi ka]an.Ashe kenan da harshe ne ake wanzar da duk wani adabin baka da ake samu,shi ke taimakawa wajen furzar da tunanin fasihi har mutane su ji, su fahimci irin }yale-}yalen jawo hankalin da ke cikin wannan aiki na adabi. Saboda haka, harshe na bayyana irin tunanin da ke cikin zukatan mutane ko kuma irin tunaninsu game da rayuwa.

**Auna Fahimta**

1. Shin me aka fahinta da Harshe?
2. Harshe na xaya daga cikin hanyoyin sadarwa. Ko an yarda?
3. Faxi abubuwa guda uku (3) da sukan zo a zuciyar Bahushe idan zai faxi magana ko hira ko zance.

## 2.4 Taqaitawa

A wannan darasi an bayyana yadda harshe yake, wannan baiwa ta hulxa a tsakanin mutum da mutum ita ta bambanta shi da sauran hallittu, ana amfani da harshe a matsayin kafa ta sadarwa, wato isar da saqo daga mai magana zuwa ga mai sauraro. Haka nan kuma, an gano cewar harshe na taka muhimmiyar rawa a matsayinsa na kafa ta bayyana tunani da falsafar al`ummar Hausawa. Domin da harshe ne ake wanzar da abubuwan da aka }ir}ira a }wa}walwa don Hausawa su fahimta su yi aiki da su. Wannan na ]aya daga cikin muhimmancin harshe, an fahinci adabin baka ba ya samuwa sai da taimakon harshen don wanzar da shi.

## 2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Harshe: Hanyar magana tsakanin al'umma iri xaya.
- Sadarwa: Isar da saqo.
- Magana: Jerin kalmomi da aka furta da baki, kuma masu ma'ana.
- Qwaqwalwa: Farin abu mai masqi-masqi a cikin qoqon kan mutum ko dabba.

## 2.6 Manazarta da Wasu Abubuwa na Qara Nazari

Lado, R. (1964): *Language Teaching* – A Scientific Approach, McGraw-Hill: New York.

Lenneberg, E. H. (1967): *Biological Foundations of Language*, Wiley, New York.

Yakasai, S A. (2012). *Jagorar ilimin Walwalar Harshe,* Sokoto. Garkuwa Media Service Ltd.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Shin me aka fahinta da Harshe?

harshe muhimmiyar kafa ce ta sadarwa cikin zamantakewa. Wato idan aka yi amfani da harshe domin sadarwa, to ko shakka babu za a samu yana ]amfare da al'ada ta hanyoyi daban-daban. Kalmomi da al'umma suke furtawa, da su ne ake bayyana al'amuran da suka shafi rayuwarsu, wato gaskiya da tunani da kuma harkoki da ake bayyanawa a matsayin tarin ilmi da sauran al'ummu ke fa'idantuwa da su. Hasali ma, kalmomi suna bayyana ]abi'ar duk wanda ya yi amfani da su cikin tadodi. Ta wannan haujin, harshe yana bayyana hanyoyin rayuwa.

**2.** Harshe na xaya daga cikin hanyoyin sadarwa. Ko an yarda?

Yin amfani da harshe wajen sadarwa tsakanin mutum da mutum na ]aya daga cikin hanyoyin da suka bambanta ]an adam dadabbobi. Duk da yake su dabbobin ma suna da tasu hanyar ta isar da sa}o a tsakaninsu, amma dai bata amfani da harshe ba. Harshe na taimakawa a fahimci sa}on da mutum yake son isarwa ga ]an uwansa. Da harshe ne ake sanar da duk abin da ake bu}atar a sanar da mutum ko don a da]a]a koya faranta, ko a ~ata ko kuma a tunzurar da zuciyar mai sauraro. Da wannan harshe ne `yan siyasa ke jan hankalin jama'a har su yadda da manufofinsu. Abubuwan da mutum ya tsara a ransa su ne sakamakon tunanin da ke cikin zuciyarsa, babu wata hanya da za a iya gane wannan tunani ko ra`ayi ba tare daya furta ba.

3. Faxi abubuwa guda uku (3) da sukan zo a zuciyar Bahushe idan zai faxi magana ko hira ko zance.

1. Darajar mai saurare a idanunsa, wato a idanun mai bayar da labarin.
2. Abin da ake maganar/hirar/ta]in ko zancen a kansa.
3. Wurin da ake gudanar da hul]o]i/ mu'amaloli.

## Kashi Na 3: Aiwatarwa

**Abubuwan da ke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Ma'anar Aiwatarwa
3.3.1 Yadda Ake Aiwatar da Adabin Baka
3.3.2 Gani da Ido
Auna Fahimta na 1
3.4 Taqaitawa
3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

Aiwatarwa ya kasance xaya daga cikin hanyoyin da ake gane adabin baka, abin da ake son mai kataru ya gane a nan shi ne duk adabin bakan da aka qirqira to wajibi ne a aiwatar dashi. Wannan aiwatarwar na iya kasancewa ta yin amfani da gavuvvan jiki ne ko harshe. Bari mu xauki rubutaccen adabi, da zarar an rubuta shi, sai dai fa a karanta ko a bayyane ko kuma a voye. Shi kuwa adabin baka galibi ana aiwatar dashi ne a lokacin da aka samar dashi. Misali in mun xauki waqar baka, ana aiwatar da waqar baka ne nan take a lokacin da ake samar da ita, idan ma an tava rereta a wani wuri, yayin da za a sake rerewa sai da a aiwatar da ita a wannan lokacin da ake wanzar da ita. Saboda haka, wannan darasi zai bayanin yadda ake aiwatarda sassan adabin baka ne don ya kasance an sami wata siffar da take bambanta adabin da sauran nau`o`in adabi.

### 3.2 Manufofin Darasi

Fatar da ake da ita a qarshen wannan darasi itace wadda za ta ba xalibai damar gane yadda ake wanzar da adabin baka, musamman waqar baka da zube nabaka da kuma wasannin kwaikwayo ko kuma zantukan hikima na baka. Misali idan waqa ce ko kuma zube na baka, ta yaya ake wanzar da su? Da me da me ake bukata wajen wanzarwar? Mene ne sakamakon da ake fatar a cimmawa yayin da aka gama wanzar da wannan adabin? Fatar mu ce mai karatu ya iya bayar da amsoshin waxannan tambayoyi a yayin da ya kammala karanta wannan darasi.

### 3.3 Ma'anar Aiwatarwa

"Aiwatarwa" na nufin yadda ake gudanar da abu" wato gwada yadda ake wani a aikace. Ida nana maganar aiwatarwa a matsayin siffa ta musanman wadda ake shaida adabin baka, to ana nufin yadda ake aiwatar da nau`o`i

ko ire-iren adabin bakan Bahaushe. Idan muka dubi yadda ake gudanar da adabin baka a aikace, musamman waqoqi, za mu ga cewa sun bambanta da yadda ake aiwatar da su a da, kafin zuwan musulunci da bayan zuwan musulunci da kuma tasirin zuwan Turawa. Misali, kamar yadda muka ambata can baya, makaxan fada ba sa kaxa wa kowa in ba jinin sarauta ba. Amma yanzu mun ga wannan al'ada ta sauya, an karya ta domin kuwa mawaqan fada na yi wa kowa da kowa waqa matuqar dai za su sami biyan bukata. Kuma idan ka kwatanta ingancin waqoqin baka na da, kafin zuwan Turawa da bayan barinsu qasar, za ka ga akwai bambanci, domin kuwa na da cike suke da gwanintar harshe, kuma ana amfani da kalmomi na ilimi da hangen nesa, amma na yanzu ba haka suke ba, mene ne dalilan da suka wanzar da haka?Babban dalilin da masana suke gabatarwa bai rasa nasaba da cewa mawaqan da suna tsayawa su shirya waqa, su tsara ta, sa`annan su tsaya a tsanake, cikin natsuwa da walwala su rera ta cikin lafazi da harshen da ya dace, tare da kixan da ya dace. Amma su na yanzu ba sa yin haka,sukan shirya waqar cikin sauri da zaquwa da tunanin abin da za a ba su, kuma babu cikakkiyar biyayya tsakanin 'yan amshi da mai ba da waqar domin akan sami inda kalaman `yan amshi kan sava da na jagorar waqa.

### 3.3.1 Yadda Ake Aiwatar da Adabin Baka

Yadda ake aiwatar da adabin baka ya dogara ne ga nau`in adabin, idan waqa ceta baka ko zube na baka galibi ana aiwatar da su ne tare da `yan amshi ko masu saurare, idan waqa ce tana zuwa haxe da kixa, wani lokaci har da `yan rawa. Makaxan ma sun bambanta domin akwai rukunan makaxan fada da na jama`a da makaxan maza da dai sauransu, su kansu kayan kixan sun bambanta. Shi kuwa zube na baka, misali tatsuniya ko qissa ko al`mara ko makamantar waxannan, ana samu masu bayar dalabari ne, wuri na musamman da aka keve haxe da masu saurare. Zantukan hikima kuwa, kusan babu wani qayyadadden lokaci ko wurin aiwatar da su. Wasanni masu siffar kwaikwayo na buqatar a yi su a aikace. Don haka, wajen aiwatar da ire-iren waxannan wasanni, misali wasannin tashe ko `yan kamanci ko wasannin gauta waxanda ake aiwatar da su lokaci-lokaci na shekara, suna buqatar kayyaki na musamman yayin da ake gudanar da su,wasu ma kamar wasannin kalankuwa da magi sukan bukaci a yi tafiye-tafiye daga wannan gari zuwa wancan garin. Wani lokaci ma rubutaccen adabi, misali kamar rubutaccen wasan kwaikwayo ba ya cika wasan kwaikwayo idan ba a aiwatar da shi a gaban `yan kallo ba.

### 3.3.2 Gani da Ido

Ya kai mai karatu, yana da kyau ka fahimci abin da ya fi muhimmancin tsakanin ganin abu da ido quru-quru da kuma karanta shi, bincike-binciken masana sun nuna cewa, xan Adam ya fi saurin fahimta da xaukar abu a qwaqwalwarsa idan ya gani da ido a bisa wanda ya karanta. Wannan bayani a bayyane yake,da zaka kwatanta fahimtar yara qanana waxanda ba su ma san ma`anar karatu da rubutu ba, da ka qara tabbatar da gaskiyar wannar maganar, duk da yake ba su je makaranta ba domin koyan karatu

da rubutu, amma kuma suna fahimta da saurin xaukar abubuwan da suka gani da idanuwansu. Bari mu xauki wani wasa guda wanda yara ke aiwatarwa, wannan wasan kuwa shi ne na `yar tsana wadda yara mata ke kwaikwayar iyayensu mata, ko kuma wasan Danda dokin kara wanda yara maza ke kwaikwayan iyayensu maza, duk waxannan wasanni ba koya wa yaran ake yi ba, hasali ma suna gani ne iyayensyu na gudanar da wannan tsarin rayuwa su kuma suka xauka. Don haka ashe ba a yi kuskure ba in an ambaci cewa gani ya kori ji. Da yawa daga cikin ire-iren adabin bakan Bahaushe ana ganinsu su da ido quru-quru a lokacin da ake aiwatar da su, Masana ilimin walwalar xan adam sun tabbatar da iqrarin da ke cewa mutane sun fi saurin fahimtar abubuwan da suka gani da idanuwansu a bisa wanxanda suka ji da kunne. Bari mu xauki misalin waqar baka, ko zube na baka ko kuma ma aiki cikin kwaikwayo, duk waxannan ana gabatar da su a gaban jam`a ne, kuma mutane suna ganin da idanuwansu quru-quru, ganin nan kuwa ko shakka babu ya kori ji.

**Auna Fahimta**

1. Me ake nufi da aiwatarwa a adabi baka?
2. Kawo wasanni guda biyu (2) da yara suke aiwatarwa ta hanyar gani da ido.
3. Yaya ake aiwatar da nau'in adabin baka na waqa?

## 3.4 Taqaitawa

Wannan darasi ya yi bayanin xaya daga cikin hanyoyin da ake gane adabin baka, wato aiwatarwa, galibi waxannan ayyukan adabin bakan ana aiwatar das u ne nan take lokacin da ake qirqirarsu. Ba kamar rubutaccen adabi ba inda sai an yi tunani an kuma tsara duk abin da ake so a rubuce. Da yawa daga cikin ayyukan adabin ana aiwatar dasu ne a lokacin da aka samar dasu, Waqar baka da zube na baka da ma wasannin kwaikwayo na baka duk suna bukatar a aiwatar da su a gaban masu kallo. Saboda haka, da zarar mai karatu ya ga wani aikin adabi, wannan hanya ta aiwatar na xaya daga cikin hanyoyin da za iya gane adabin baka ne ko kuma wani nau`in adabin ne daban.

## 3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Qissa: Labari ne na gaskiya ba almara ba, kamar labarin wasu annabawa.
- Adabin baka: Nau'in adabi da Hausawa suka gada tun kaka da kakanni.
- Rubutaccen adabi: Nau'in adabin da ya samu sakamakon zuwan Turawa
- Zube: Qananan labarai da ke zuwa kara zube ba tare da wasu qa'idoji ba.

### 3.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Okpewho, I. (1990). *Oral Performance in Africa*. Ibadan Spectrum Books. Ltd.

…………. (1992). *African Oral Literature*. Bloomington IN Indiana University Press.

### 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ake nufi da aiwatarwa a adabin baka?

Aiwatarwa na nufin yadda ake gudanar da abu" wato gwada yadda ake wani a aikace. Idan na maganar aiwatarwa a matsayin siffa ta musanman wadda ake shaida adabin baka, to ana nufin yadda ake aiwatar da nau`o`i ko ire-iren adabin bakan Bahaushe.

2. Kawo misalin wasanni guda biyu (2) da yara suke aiwatarwa ta hanyar gani da aido

Ga wasanni guda biyu da yara ke aiwatarwa, wannan wasan kuwa shi ne na `yar tsana wadda yara mata ke kwaikwayar iyayensu mata, ko kuma wasan Danda dokin kara wanda yara maza ke kwaikwayan iyayensu maza, duk waxannan wasanni ba koya wa yaran ake yi ba, hasali ma suna gani ne iyayensyu na gudanar da wannan tsarin rayuwa su kuma suka xauka. Don haka ashe ba a yi kuskure ba in an ambaci cewa gani ya kori ji.

3. Yaya ake aiwatar da nau'in adabin baka na waqa?

Yadda ake aiwatar da adabin baka ya dogara ne ga nau`in adabin, idan waqa ceta baka ko zube na baka galibi ana aiwatar da su ne tare da `yan amshi ko masu saurare, idan waqa ce tana zuwa haxe da kixa, wani lokaci har da `yan rawa. Makaxan ma sun bambanta domin akwai rukunan makaxan fada da na jama`a da makaxan maza da dai sauransu, su kansu kayan kixan sun bambanta.

**Kashi Na 4: Ji da Gani**

**Abubuwan da ke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Ma’anar Ji da Kunni
4.3.1 Dame Ake Ji
4.3.2 Ganewa
4.3.3 Hoton Zuci
Auna Fahimta na 1
4.4 Taqaitawa
4.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
4.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 4.1 Gabatarwa

Wannan darasi na bayanin wata hanya ta musanman da ake iya gane adabin baka. Kurma yana son ya yi magana da mutane, haka nan makaho yana son ya gansu, shi kuwa bebe so yake ya ji abin da suke faxi. Wannan ya nuna mana cewa idan an ji abu da kunne, to ko shakka babu an furta wata kalma. Saboda haka ayyukkan adabin baka furta su ake yi da taimakon harshe mutane na saurare da kunne, ashe adabi ne daba karanta shi ake yi ba. Don duk inda aka ga wata fasaha ko hikima wadda ta jivanci harshe kuma an yi tada baka ta zama adabin baka. A wannan darasi za a bayyana ma'anar ‘ji’ da yadda ake iya shaida abubuwan da aka ji da kuma irin sakamakon da ke biyo wa baya a sanadiyyar wannan ‘ji’ da yadda jin ke haifar da tunani.



## 4.2 Manufofin Darasi

Wannan darasi na da manufofin da yake qoqarin cimmawa yayin da aka kammala karatu kamar haka:

- Ma'anar Ji da Kunni
- Ganewa idan an ji Kunni
- Hoto gurbi a Zuciya



## 4.3 Ma’anar Ji da Kunni

Da jin sunan an san cewa saurare ake nufi, saboda haka za a ji abubuwan da mutane ke faxi ne. Idan aka ce ‘Ji’ da kunni to ana nufin ' yin shiru ko tsit don a ji magana' ko kuma ' yin tsumayi ko dakace ko jiran wani mutum ko wani abu'. Sannan akwai kalmar 'saurara' wadda aka bayyana ma'anarta da 'kasa kunne da niyyar jin sauti' ko kuma 'Tsumayi ko dakata

ko jira'. Qamusun Hausa (2006:394). To a wannan varayi ana magana ne a kan ji da kunni na nau`o`in adabin baka. Idan aka ce wane baya jin magana, akwai fassara iri biyu: da farko dai ma`anar zata iya kasancewa ana nufin shi kurma ne, haka nan kuma wata ma`anar za ta iya nufin baya aikata abubuwan da suka kamata ko kobaya aikata abubuwan da aka umurce shi daya yi. Duk waxannan basu muke magana a nan ba, 'Ji' da muke magana a a nan shi ne wanda ya jivanci sauraren zantukan hikiman Bahaushe.

### 4.3.1 Dame Ake Ji

Tun daga bayyana ma'anar 'Ji'za a iya fahimtar cewa ana saurare ne da kunne sa`annan a ji abubuwan da aka faxa ko fahimtar sauti ko qarar da aka ji. Qamusun Hausa (2006:254) ya ce kunne shi ne: "Sashen jiki da ke saman kunci wanda ake jin sauti." Shi kuma sauti na iya kasancewa na magana ko wani abu daban, kamar qarar kixa ko faxuwar wani abu ko motsa wani abu da sauransu ba iyaka.

### 4.3.2 Ganewa

Ana gane adabin baka idan an saurari hikimomi da fasahar al`umma an kuma gane abubuwan da suke nufi kosaqon da suke isarwa. Ganewa dai na nufin 'fahimta' ko 'sani' wanda kan faru a yayin da kunne ya Ji sautin wani abu, take sai ya aika wa qwaqwalwa wadda ita ke da alhakin xaukar nau'in saqon da ya iske ta. Daga nan wani sashen qwaqwalwa zai xauki aikinsa na sarrafa wannan saqon sautin har a samu fahimtar wannan sauti.
Gane batun da aka ji zai iya xaukar fuskoki daban-daban kamar haka:
Idan mutum ya ji wani sauti zai qoqarin fahimtar ko wane irin qara ko sauti kunnensa ya ji. Shin sautin magana ne ko kukan wata dabba ko wani abu daban. Idan sautin magana ne, zai iya fahimtar wannan muryar namiji ne ko mace, babba ko yaro da sauransu. Sannan sautin maganar nan ihu ne ko kuka ko magana sosai ko waqa ce ko tasuniya? Idan kuma sauti ne irin na dabba, to wanda ya ji zai fahimci kukan wace dabba ce kunnensa ya ji.
Saurin gane adabin baka ya dogara ga irin nau`in adabin, mai saurare kan qoqarta fahimtar saqon sautin da kunnensa ya ji ba tare da ya yi dogon tunani ba. Misali, yayin da mutum ya ji wata waqar baka ko wani nau`in zube nabaka misali: "Ga ta nan ga ta nanku" zai yi saurin gane cewa tatsuniya za a gabatar. Ko kuma waqa ce ake rerawa, gane nau`in adabin shi ke bayar da dammar fahimtar abubuwan da aka ji da kunni aka kuma gane saqon da ake fatar a isar ga jama`a.
A wani qaulin kuwa, yanayin sauti ko maganar da mai saurare ya ji da kunnensa na iya haifar masa da fahimtar da lallai dole sai ya nemi fassara ko qarin bayani. Misali idan mai saurare ya ji wasu fasahar baka, kamar karin magana ko habaici cikin zance, mafi yawanci sai ya buqaci fassara ko qarin bayani.
Sa`annan kuma abin da kunne ya ji, yakan haifar da fahimta mai tasirantar zuciya. Misali, idan mai sauraro ya ji kuka ko dariya, dole ya ji xarsashin baqin ciki ko zullumi ko tausayi ko farin ciki a zuciyarsa domin ya gane abin da sautin ke nufi.

### 4.3.3 Hoton Zuci

Sakamakon sauti ko qara ko maganar da mutun ya ji kan haifar da sura ko hoton wannan abu a cikin zuciyar mai saurare. Hoton abu na samuwa ne a yayin da aka saurari wata qara ko sauti, sai qwaqwalwar mai sauraron ta sarrafa ganin wannan siffar abin da aka ji. Kamar mutum ne ya ambaci wasu kalmomi ko zantuka na hikima a waqa ko zube ko wani nau`in adabin baka, zuciya kan ayyana hoton wannan abu harta bashi wasu siffofi da matsuguni na fahimta a cikin zuciya. Kalmomin adabin baka cike suke da hikimomi da fasahar da wani lokaci sai an yi wa mutum bayanin ga abin da ake nufi. Hanya mafi sauqi ta gane adabin baka ita ce ta sanin cewa a wasu lokuta ba ma`ana ta zahiri ake dubawa kaxai ba a kalmomin adabi, har ma da ma`ana ta voye.Misali, idan aka ji qarar mutsuttsuka takarda, kila kuxi ake qirgawa ko kuma wata takardar karatu ake motsawa. Idan qirgar kuxi ne, da ma za a yi magana da ta dace da wannan aiki. A irin wannan yanayi, mai sauraro sai ya riqa ganin kuxin kamar da gaske yake kallo. Tamkar a waqar baka, inda mawaqi kan siffanta wani abu dangane da kyau ko muninsa ko girmansa ko qarfinsa da sauransu, dole ne mai saurare tunaninsa ya yi saurin sarrafuwa har ya ga hoton abin da ya ji ana siffantawa. Ko ma ba siffantawa aka yi kai tsaye ba, akwai maganar da za ta iya tilasta wa mai saurare ganin hoton abin da aka ambata. Misali, a cikin waqar baka Barmani Coge da ta ce:

> Kuma an je wurin barka
> Ga uwargida bisa wundi
> Xayar a kan `yar kanti,
> Da wadda ba ta sana'a
> Ta xauki guntun keso
> Ta kakkave shi ta zauna.
> (Rabi 2011)

Duk kunnen da ya ji wannan, to babu shakka sai tunaninsa ya xauka ya sarrafu ta yadda zai ga hoton mata uku waxanda suka je barkar haihuwa, kuma kowacce da irin shigarta da irin nau'in tabarmar da suka zauna a kai. Haka lamarin ke kasancewa a tatsuniya, domin tana qunshe da maganganu masu tilasta tunanin mai sauraro a tafarkin ganin hoton abin da ake magana a kai.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar 'ji' a matsayin siffa ta shaida adabin baka.
2. Da wane sashe na jikin xan Adan ake ji?
3. Yaya ake bayyana hoton zuci a waqar baka?

### 4.4 Taqaitawa

'Ji' da kunne kamar yadda aka fahimta siffa ce babba wadda ake amfani da ita wajen gane adabin baka saboda kasancewar adabin baka kamar yadda sunan ya nuna, da baka ake wanzar da shi kuma da kunne ake ji da fahimtar abubuwan da aka saurara. A lokacin da ake aiwatar da adabin

baka dole ana bukatar masu saurare, misali idan ana waqa ko tatsuniya da sauran nau'o'in adabin baka dole akwai masu ji da kunni domin su fahimci abubuwan da ake qoqarin isarwa garesu. Wannan ya sa aka bayyana ma'anar kalmar ‘ji; da kuma abin da ake ‘ji’ da shi tare da fito da sakamakon da ake iya samu idan an yi ‘ji’ qara ko sauti ko makamancin waxannan, wato ganewa da samar da hoton abin a cikin zuciya.

**4.5 Ma’anar Wasiu Muhimman Kalmomi**

- Ji: Sauraron sauti ko amon wani abu.
- Siffa: Hanyar bayyana kamannin wani abu.
- Tatsuniya: Qagaggen labari da magabata suke yi w ayara domin koya masu dabarun zaman duniya.
- Waqa: Tsararriyar magana da ake rerawa a kan kari ko rauji.

**4.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari**

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Rabi, M. (2011): “Xabi’un Mata a Bakin Mawaqan Baka na Hausa” Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsuna da Al’adun Afrika, Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

**4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar ‘ji’ a matsayin siffa ta shaida adabin baka.

Idan aka ce ‘Ji’ da kunni to ana nufin ' yin shiru ko tsit don a ji magana' ko kuma ' yin tsumayi ko dakace ko jiran wani mutum ko wani abu'

2. Da wane sashe na jikin xan Adam ake ji?

Tun daga bayyana ma'anar ‘Ji’za a iya fahimtar cewa ana saurare ne da kunne sa`annan a ji abubuwan da aka faxa ko fahimtar sauti ko qarar da aka ji. Qamusun Hausa (2006:254) ya ce kunne shi ne: "Sashen jiki da ke saman kunci wanda ake jin sauti." Shi kuma sauti na iya kasancewa na magana ko wani abu daban, kamar qarar kixa ko faxuwar wani abu ko motsa wani abu da sauransu ba iyaka.

3. Yaya ake bayyana hoton zuci a waqar baka?

A waqar baka, inda mawaqi kan siffanta wani abu dangane da kyau ko muninsa ko girmansa ko qarfinsa da sauransu, dole ne mai saurare tunaninsa ya yi saurin sarrafuwa har ya ga hoton abin da ya ji ana siffantawa. Ko ma ba siffantawa aka yi kai tsaye ba, akwai maganar da za ta iya tilasta wa mai saurare ganin hoton abin da aka ambata.

## RUKUNI NA 3: YAYA AKE TATTARA ADABIN BAKA?

### Kashi Na 1: Matsalar Rubutu

### Abubuwan da ke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Ma’anar Rubutu
1.3.1 Waxanne Abubuwa ne ake Rubutu a kai?
1.3.2 Rashin Tawada
1.3.3 Adana a ‘Ka’
Auna Fahimta na 1
1.4 Taqaitawa
1.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Adabin baka adabi ne da yake a ka wanda ake yi don a saurara amma kuma in an zo ana son a tattara shi akwai hanyoyin da ake bi a tattara shi. To ga irin fasalce-fasalcen da za a bi a tattara shi, da yawa daga cikin adabin baka ana wanzar das u tab aka daga wannan mutum zuwa wancan, don haka akwaik matsala ta rashin rubutu. Matsalar iya rubutu ko sifanta tunani a rubuce ita ce babbar matsalar da aka danganta ta da adabin baka wadda wannan kashi zai tattauna a kai. Duk hikimomin da fasahar baka waxanda baqar fata suka samar ba a xauke a matsayin adabi ba saboda matsalar ba a rubuta su ba. Don haka za a bayyana ma'anar rubutu da abubuwan da ake amfani da su wajen yin rubutu da matsalar da ke tattare da su.



### 1.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce, ana so almajirai su fahimci cewa tattaara adabin bakan Bahaushe na da babbar matsala saboda rashin rubutu tun farkonsa har ya zuwa yau. Shi ya sa ake so almajirai su san waxannan:

a- Ma'anar rubutu
b- Abubuwan da ake rubutu a kai
c- Matsalar tawada
d- Adana

## 1.3 Ma’anar Rubutu

Tattara adabin baka ya qunshi bayanai da aka samu ta baka kuma ba rubuta su ake yi ba, za a fi gane abin da ake nufi idan an yi bayani ma`anar rubutu. Qamusun Hausa (2006:374) ya bayyana ma’anar kalmar ‘rubutu’ da cewa shi ne: “Zanen magana a kan takarda ko allo ko a wani bigire.” Wani shihin malamin kuwa, Malumfashi (2019:1), ya bayyana ma’anar rubutu da cewa: “Wata kafa ce ta mayar da tunani ko harshe a cikin takarda.” Sai dai cikin bayanansa, an fahimci cewa rubutu ba lallai sai a kan takarda ba domin wannan sanance ne na baya-baya tunda an tabbatar da cewa rubutu fasaha ce ta kowace al’umma a doron qasa. Sai dai kowace al’umma da abin/abubuwan da take amfani da shi/su wajen yin rubutu savanin takarda.

### 1.3.1 Waxanne Abubuwa ne ake Rubutu a kai?

Masana sun bayana ire-iren abubuwan da ake rubutu a kansu kafin a sami takarda. Rubutu ya kasance ana yin sa a kan abubuwa da dama in an xebe sanannen abun da aka fi sani a yau, wato ‘takarda’. Malumfashi, (2019:1) ya bayyana cewa: “Kowace al’umma a doron qasa da irin nata yanayin rubutun, ba dole sai a takarda ba; wasu na yin sa a jikin kogo ko itace ko ganyaye ko fatu ko duwatsu. Wasu al’ummomi kuma ta alamci ko nuni ko sassaqe-sassaqe ko makamantan haka da ake ganin ajiyayyen tunaninsu ko harshensu, wasu kuma ta hanyar kixa ko waqa ko hito ko wani dabashiri da suka tanada domin tallafar nasu tunanin ko harshen.”
Hausawa suna daga cikin al’ummomin da suka yi rubutu a kan wasu abubuwa kafin zuwan takarda a gare su. Abubuwan da suka yi wani rubutu a kai akwai duma, da fatun dabbobi da kuma tsaga a jikin fatar mutum wadda ake kira tsagar gargajiya da kuma a kan allo wanda ake sassaqa shi daga itace. Duka alamomi ne waxanda ke bayyana wani tunani na al’umma a wancan zamani dangane da bambance-bambancen garuruwa da abin da ya shafi sana’o’i da sauransu.

### 1.3.2 Rashin Tawada

Kalmar tawada tana da ma’anoni kamar uku a Qamusun Hausa (2006:434), amma wadda ake nufi a nan ita ce wadda aka ce: “Baqin ruwa mai kauri wanda ake tsoma alqalami ana rubutu da shi.”
Bisa fahimta, ita tawada tana nufin ruwan rubutu wanda akan tanada musamman daga wasu nau’o’in itace kamar xinya, a haxa da wasu sinadarai kamar qaro a dafa har a samar da ita galibi baqa qirin a launinta, amma akwai ta icen xinya da launinta ke kama da ruwan zuma mai duhu. Idan an fahimci ko mece ce tawada, to sai a komo ga bayanin matsalarta a fagen adabin bakan Bahaushe. Kamar yadda aka sani, amfani da tawada a yi rubutu daga baya ya shigo wa rayuwar Hausawa, yayin da su kuma sun daxe suna wanzar da adabinsu da baka ne. Idan sun wanzar da adabin nasu kuma suna adanawa ne a ‘ka’ ba a rubuce ba. ko a lokacin da addini ya samu qarfi a qasar Hausa, an yi amfani da tawada ne mafi akasari wajen koyar da addinin Musulunci. Ko da aka samu waqoqi ma, babu na baka

da aka rubuta, balle a samu sauran fannonin adabin baka irin su tatsuniya da azancin maganganu da sauransu.

### 1.3.3 Adana a 'Ka'

A Qamusun Hausa (2006:2) an bayyana ma'anar 'adana' da cewa shi ne: "Ajiye abu yadda ba zai salwanta ko ya lalace ba." Dangane da adabin bakan Bahaushe adana matsala ce tun asali da ta sa ximbin ayyukan adabin Bahaushe suka salwanta. Kamar yadda aka sani, ana adana adabin baka ne tun farko a 'ka'. Daga baya zamani ya kawo sauyi inda ake iya adana adabin baka a rubuce ko a cikin fayafayen sidi da kaset-kaset da sauran hanyoyi irin na zamani. Duk da haka, in an ga adabin baka ya adanu to ta fuskar nazarce-nazarce ne ko kuma a samu a gidajen rediyo. Su ma xin akwai sakaci sosai na rashin tattala kayayyakin da ke xauke da adabin bakan yadda ya kamata.

**Auna Fahimta**

1. A bisa waxanne abubuwa Hausawa sukeyin rubutu kafin su sami takarda?
2. Yi cikakken bayanin abin da ka fahinta da tawada da yadda rashin ta ya haifar da rashin rubutu ga mutanen Afirka.
3. Adana na daga cikin matsalolin adabin baka. Yaya abin yake?



## 1.4 Taqaitawa

Wannan darasi ya duba yadda za iya tattara adabin baka ta hanyar magance ire-iren matsalolin da ke tattare da samar da adabin baka, an gwada cewa Turawa sun qyamaci hikimomi da fasahar baka ta al`ummar afirka ba don komi ba sai don ba a rubuce suke ba. Matsalar farko da wannan darasi ya duba ita ce ta rashin rubutu. Ba za a kira mutumin da bai iya rubutu da karatu jahili ba, domin ilimi a qwaqwalwa yake kuma hanyar wanzarwa tana iya kasancewa ta baka ko ta rubutu. Haka nan kuma, darasin ya duba ire-iren abubuwan da ake yin rubutu a kansu waxanda mutanen da suka yi amfani da su. Daga nan, an duba matsalar rashin tawada da ta adana a matsayin matsalolin da ke tattare da adabin baka.

## 1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Tawada: Baqin ruwa mai kauri wanda ake tsoma alqalami ana rubutu da shi.
- Ilimi: Yin sani musamman a fannin addini ko kuma a ilimin zamani.
- Karatu: Karanta abu daga littafi ko takarda ko allo.
- Rubutu: Zanen magana a kan takarda ko alli ko wani bigire.

## 1.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Malumfashi, I. (2019): “Kunnenka Nawa? Labarin Hausa a Rubuce” a Cikin *Labarin Hausa a Rubuce1927-2018* ISSBN: 978:978-55352-8-0. Zariya: Xab’in Maxaba’ar Jami’ar Ahmadu Bello.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. A bisa waxanne abubuwa Hausawa sukeyin rubutu kafin su sami takarda?

Hausawa suna daga cikin al’ummomin da suka yi rubutu a kan wasu abubuwa kafin zuwan takarda a gare su. Abubuwan da suka yi wani rubutu a kai akwai duma, da fatun dabbobi da kuma tsaga a jikin fatar mutum wadda ake kira tsagar gargajiya da kuma a kan allo wanda ake sassaqa shi daga itace. Duka alamomi ne waxanda ke bayyana wani tunani na al’umma a wancan zamani dangane da bambance-bambancen garuruwa da abin da ya shafi sana’o’i da sauransu.

2. Yi cikakken bayanin abin da ka fahinta da tawada da yadda rashin ta ya haifar da rashin rubutu ga mutanen Afirka.

Bisa fahimta, ita tawada tana nufin ruwan rubutu wanda akan tanada musamman daga wasu nau’o’in itace kamar xinya, a haxa da wasu sinadarai kamar qaro a dafa har a samar da ita galibi baqa qirin a launinta, amma akwai ta icen xinya da launinta ke kama da ruwan zuma mai duhu. Dangane da matsalarta a fagen adabin bakan Bahaushe kuwa, kamar yadda aka sani, amfani da tawada a yi rubutu daga baya ya shigo wa rayuwar Hausawa, yayin da su kuma sun daxe suna wanzar da adabinsu da baka ne. Idan sun wanzar da adabin nasu kuma suna adanawa ne a ‘ka’ ba a rubuce ba. ko a lokacin da addini ya samu qarfi a qasar Hausa, an yi amfani da tawada ne mafi akasari wajen koyar da addinin Musulunci. Ko da aka samu waqoqi ma, babu na baka da aka rubuta, balle a samu sauran fannonin adabin baka irin su tatsuniya da azancin maganganu da sauransu.

3. Adana na daga cikin matsalolin adabin baka. Yaya abin yake?

Dangane da adabin bakan Bahaushe adana matsala ce tun asali da ta sa ximbin ayyukan adabin Bahaushe suka salwanta. Kamar yadda aka sani, ana adana adabin baka ne tun farko a ‘ka’. Daga baya zamani ya kawo sauyi inda ake iya adana adabin baka a rubuce ko a cikin fayafayen sidi da kaset-kaset da sauran hanyoyi irin na zamani. Duk da haka, in an ga adabin baka ya adanu to ta fuskar nazarce-nazarce ne ko kuma a samu a gidajen rediyo. Su ma xin akwai sakaci sosai na rashin tattala kayayyakin da ke xauke da adabin bakan yadda ya kamata.

## Kashi Na 2: Wurin Masu Shekaru

**Abubuwan da ke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Ma’anar Tsufa
2.3.1 Yadda Tsufa Take Tasiri ga Bayani
2.3.2 Riqe Abu
2.3.3 Sauye-Sauye
Auna Fahimta na 1
2.4 Taqaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Galibi an fi samun wasu nau`o`in adabin baka a wurin tsofaffi da waxanda suka manyanta. Wasu nau`o`in adabin baka abubuwa ne waxanda suka daxe waxanda aka gada tun kaka da kakanni, wasu daga ciki ma ba a iya qayyade lokacin da aka fara samar da su. Saboda haka ana iya samun matsala wajen shekarun da aka yi shi da gane shi da fahimtar sa baki xaya. Sa`annan waxanda aka yi a shekara dubu da suka wuce za su sha bamban da waxanda aka yi shekar xari biyar, da waxanda aka yi shekara xari da waxanda aka yi a yanzu. Sa`anna wajen taho shi kuma za a cancanza waxansu abubuwa, wasu abubuwa za su cancanza. Kayan cikin na iya cancanzawa domin su dace da yadda al`umma take da yadda zamani yake. Misali kamar mu xauki abinci a tatsuniyar Ruwan Bagaja, za mu ga cewa ire-iren kogin abincin da aka ambata suna canzawa a yanzu, idan yanzu ne za rinqa jin ana ambaton kogin Indomi da Shawarma da sauransu maimakon koguna tuwon shikkafa da alkama da aka yi amfani da su a tatsuniyoyin can baya. Tsufa ko shekaru xaya ne daga cikin batutuwan da suke kawo tarnaqi ga adana adabin baka. Wannan kashi ya qunshi bayanai kan ma’anar tsufa da yadda tsufa ke tasiri ga bayani har ta haifar da gushewar riqe abu da kuma kwan-gaba-kwan-baya.



### 2.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce xalibai su fahimci ana tattara adabin baka ne ta tuntuvar tsofaffi, kuma tsufa na xaya daga cikin matsalolin tattara adabin baka.. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai za su fahimci:

- Ma’anar tsufa
- Yadda Tsufa ke tasiri ga bayani
- Bayyana tsufa ke haifar da gushewar gane abu da kwan-gaba-kwan-baya.

## 2.3 Ma'anar Tsufa

Tsufa na nufin kaiwa munzalin tsoho, wato a tsofe ko a daxe a duniya, (CNHN, 2006 : 459). Kenan, tsawon lokacin da mutum ya kai a raye ko daxewarsa a doron qasa shi ke haifar da tsufa gare shi. Wanda ya daxe a duniya kuma shi ne tsoho, mace kuma tsohuwa, jam'i tsofaffi. Shekarun tsufa suna farawa ne daga shekara sittin zuwa sama. Masu adadin waxannan shekaru sukan kasance masu rauni saboda jikinsu ya yi sanyi, shekarun sun ja, tunaninsu ya raunata. Domin haka riqe abu yana yi masu wahala.

### 2.3.1 Yadda Tsufa Take Tasiri ga Bayani

Bayanan da ake samu daga tsofaffi na adabin baka ba rubuce suke ba, duk bayanin da ba a rubuce yake ba, wato yana 'ka' ne, an haddace shi a qwalqwalwa, yakan iya fuskantar tasgaro lokacin da tsufa ya zo, domin qwaqwalwar da ta riqe bayanin ta yi rauni sakamakon tsawon lokaci. Shi ya sa idan aka iske tsoho ko tsohuwa domin neman wani bayani game da wani nau'in adabin baka, za a iske akwai givi a wasu bayanan sakamakon tsufa ta sanya ba komai qwaqwalwar za ta iya riqewa ba, in ma ta riqe xin a da, to tsufa ya sanya bayanin ya sami tasgaro.

### 2.3.2 Riqe Abu

Bayanan da ake samu wurin tsofaffi ya samu ne sakamakon iya riqe abubuwa a ka da Allah ya ba bayinsa. Da yawa daga cikin adabin baka sun sami ne daga wannan al`ummar da suka gabata zuwa `ya `ya da jikoki. Saboda haka tsufa kan haifar da gushewar riqe abu ta yadda abin da qwaqwalwa ta haddace tsawon lokaci za a iya mantawa da shi saboda halin jiki da jini. Mantuwa siffa ce daga cikin siffofin tsufa kuma xabi'a ce da ake samun galibi tsofaffi da ita. Shi ya sa za a iya tattaunawa da tsoho ko tsohuwa yanzun nan, in an jima kaxan ya manta, ko an tayar masa da batun za a sha fama kafin ya tuna. Irin wannan xabi'a tana shafar adabin baka, shi ya sa abin da aka riqe a ka, game da adabi, zai iya gushewa lokacin da tsufa ta zo.

### 2.3.3 Sauye-Sauye

Mai tattara adabin baka sai ya kula da sauye-sauyen da zai iya samu yayin tattara wani nau`in adabin. Yanayin wata waqar sai ta bambanta daga bakin mai ruwaito ta idan suna da yawa , haka nan kuma, tana iya bambanta daga wuri zuuwa wuri. Idan a wurin tsofaffi ne ake neman bayanai ta afa sani tsufa kan haifar da kwan-gaba-kwan-baya wajen bayani kan adabin da ke riqe a qwaqwalwa. Saboda yanayi na tsufa da shekaru masu yawa a doron qasa da ke haifar da raunin qwaqwalwa, akan sami harxewar bayani a kan aikin adabi, wato yayin da ake bayani a kan wani abu na adabi, sai an yi nisa sai a dawo farko, can kuma a tsallaka wani vangaren, in an xinke nan a valle nan, haka dai a yi ta kwan-gaba-kwan-baya. Wannan duk tsufa ce take haifar da hakan.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana yadda tsufa ke zama tarnaqi wajen tattara adabin baka.
2. Waxanne irin sauye-sauye aka iya samu wajen tattara adabin baka daga wancan zamani zuwa wannan zamanin?
3. Adadin shekara nawa ne tsufa yake farawa?

## 2.4 Taqaitawa

Wannan kashi ya yi bayanin muhimmancin tattara adabin baka wurin waxanda suke da yawan shekaru, haka nan kuma, duk da yake ana samun bayanai na adabin baka daga waxanda suka manyanta, wannan ba shi zai hana samun wasu matsaloli da suka haxa da tsufa da sauye-sauyen da za iya samu na ayyukan adabin ba. Irin haka na faruwa ne kasancewar wasu ayyukan sun daxe kuma an sami sauyi na zamani da ire-iren abubuwan da mutane ke amfani da su. Bahaushe na cewa idan kixa ta canza rawa ma kan canza. Wato idan zamani ya canza to zai iya shafar ire-iren ruwaito adabin da ake samu domin za a bayar da su ne dai dai da irin abubuwan da waxannan mutane suke amfani da su.

## 2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Sauyi: Canji ko juyi.
- Tsufa: Kaiwa mitsanin tsoho, ko kuma daxewa a duniya.
- Zamani: Lokaci ko kuma yayi
- Tasiri: Muhimmanci ko dangantaka ko qarfin wani abu a kan wani.

## 2.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Bayyana yadda tsufa ke zama tarnaqi wajen tattara adabin baka.

Bayanan da ake samu daga tsofaffi na adabin baka ba rubuce suke ba, duk bayanin da ba a rubuce yake ba, wato yana 'ka' ne, an haddace shi a qwalqwalwa, yakan iya fuskantar tasgaro lokacin da tsufa ya zo, domin qwaqwalwar da ta riqe bayanin ta yi rauni sakamakon tsawon lokaci. Shi ya sa idan aka iske tsoho ko tsohuwa domin neman wani bayani game da wani nau'in adabin baka, za a iske akwai givi a wasu bayanan sakamakon tsufa ta sanya ba komai qwaqwalwar za ta iya riqewa ba, in ma ta riqe xin a da, to tsufa ya sanya bayanin ya sami tasgaro.

2. Waxanne irin sauye-sauye aka iya samu wajen tattara adabin baka daga wancan zamani zuwa wannan zamanin?

Mai tattara adabin baka sai ya kula da sauye-sauyen da zai iya samu yayin tattara wani nau`in adabin. Yanayin wata waqar sai ta bambanta daga bakin mai ruwaito ta idan suna da yawa , haka nan kuma, tana iya bambanta daga wuri zuuwa wuri. Idan a wurin tsofaffi ne ake neman bayanai ta afa sani tsufa kan haifar da kwan-gaba-kwan-baya wajen bayani kan adabin da ke riqe a qwaqwalwa. Saboda yanayi na tsufa da shekaru masu yawa a doron qasa da ke haifar da raunin qwaqwalwa, akan sami harxewar bayani a kan aikin adabi, wato yayin da ake bayani a kan wani abu na adabi, sai an yi nisa sai a dawo farko, can kuma a tsallaka wani vangaren, in an xinke nan a valle nan, haka dai a yi ta kwan-gaba-kwan-baya. Wannan duk tsufa ce take haifar da hakan.

3. Adadin shekara nawa ne tsufa yake farawa?

Tsufa na nufin kaiwa munzalin tsoho, wato a tsofe ko a daxe a duniya. Shekarun tsufa suna farawa ne daga shekara sittin zuwa sama. Masu adadin waxannan shekaru sukan kasance masu rauni saboda jikinsu ya yi sanyi, shekarun sun ja, tunaninsu ya raunata. Domin haka riqe abu yana yi masu wahala.

**Kashi Na 3: Kulawa da Tanaden-Tanaden Al'ada**

**Abubuwan da ke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Ma'anar Al'ada
3.3.1 Al'adun Al`umma
3.3.2 Sauye-Sauyen Al'adu
Auna Fahimta na 1
3.4 Taqaitawa
3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 3.1 Gabatarwa

Tsarin al`ada da sauye-sauyen da ke fuskantar al`adun Hausawa suna iya shafar yadda za a tattara adabin baka, saboda haka, wannan darasi ya duba ma`anar al`ada da kuma yadda al`adun Hausawa kan iya zama cikas wajen tattara adabi bai xaya. Za a duba bayanan da masana suka yi kan al`ada, an kuma tsaya ga fannoni guda uku muhimmai na al`ada, wato Aure da haihuwa da mutuwa. A cikin an xan zaqulo wuraren da ake jin za su iya haifar da cikas wajen tattara ayyukan adabin baka na Bahaushe.

## 3.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce xalibai su iya gane ko me ake nufi da al`ada da kuma muhimman vangarorin al`ada. Wajen gudanar da waxannan al`adu ne ake samun shigar gizai gizai na adabin baka. Misali a cikin al`adar aure ake samun kaxe-kaxe da waqe-waqe na samari da `yan mata. Don haka ta yaya al`ada za ta iya zama cikas wajen tattara ayyukan adabin baka? Gano amsarita ce manufar wannan darasin.

## 3.3 Ma'anar Al'ada

Masana sun gwada cewa wannan kalma tun farkontaba Bahaushiyar kalma ba ce, tun usuli aro ta Hausawa suka yi daga Larabci. Sai dai kuma, ganin cewa are-aren kalmomi tsakanin Hausa da Larabci da]a]]en al'amari ne a tarihi (Ibrahim, 1982) ya sa ba za mu bi diddigin tarihin ba. Duk da haka, a luggar Larabci, al'ada na nufin wani abin da aka saba yi ko ya saba wakana ko aka riga aka san da shi. Da wannan dalili ne wasu masana furu'a ke gabatar da wani zancen hikima mai cewa "*Al'adatul baladi kas sunnah*" wato al'adar da gari ya saba da ita kamar sunnah ce (Bunza, 2006).

A harshen Hausa kuwa, masana sun kalli al'ada da ma'anoni mabambanta. Bunza (2006) cewa ya yi 'Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar ]an Adam tun daga haihuwarsa zuwa kabarinsa'. Wato a ko'ina mutum ya samu kansa, duk wata ]abi'a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu, ko yake rayuwa, ita ce al'adar da za ayi musu hukunci da ita. Saboda haka, babu wata al'umma da za ta rayu a doron }asa face tana da al'dar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata al'ummar daban.
Shi kuwa Taylor (1871) ya bayyana ma'anar al'ada da cewa 'Al'ada ta }unshi dukkan abubuwan da al'umma ke yi wa]anda suka ha]a da ilmi da imani da fasaha da }ere}ere da tarbiyya da horo da hani da sauran wasu halaye da ]an-Adam ke yi a matsayinsa na ]an-Adam'. Sai kuma Gidden (1989) mai ganin 'Al'ada a matsayin ]abi'o'in kirki wa]anda al'umma ta aminta da su da horo da hani da nisha]antarwa da irin }ere-}eren da al'umma ke yi da hannunta.
Ma'anar al'ada ga masana al'ada ba ta wuce "Wata tsararriyar kimiyyar rayuwar mutane tun daga haihuwarsu har zuwa kabarinsu ba, falsafar al'ada da kimiyyarta ya qunshi fasahar mutane da aqidojinsu da taskar ayyukan da suke sarrafawa da hannayensu da bakunansu, da gavvansu da abubuwan da suka yi imani da su. Waxannan abubuwan an gaje su ne, ko qirqiro su aka yi, ko an garwaya su da wasu baqin al'adu, duk suna cikin hurumin nazarin al'ada". Bunza, (2011:2).Al`ada ita ce abubuwan da mutum ya saba yi, yau da gobe,akwai al`adu da dama waxanda Hausawa ke yi waxanda suka shafi zamantakewa. A ciki za iya samun wasu abubuwa waxanda ka iya zama matsala wajen tattara adabin baka. Misali idan ana buqatar bayanin ire-iren waqen da mata ke yi ko surkullen da suke yi wajen haihuwa, ba dole ne a sami cikakken bayanin abin da ake so ba.

### 3.3.1 Al'adun Al`umma

Al`adar wani garin ta bambanta da ta wani garin, duk da yake akwai inda ake tarayya, amma bambancin al`ada kan shafi ingancin tattara adabin baka. Sa`annan kuma idan an lura da yadda al`adar wuri yake, yakan bayar da haske na yadda za a tattara adabin baka na wannan wuri, a qasashen Hausa yanayin tsarin al`ada da xabi`u kusan duk xaya ne in ban da `yan bambance-bambance. Tattara adabin baka a qasar Hausa ba wasu matsaloli gare su waxanda za su haifar da rashin ingancin adabin baka, bayanai sun gabata kan ma`anar al`ada, kuma daga abubuwan da muka fahinta, za a fahimci cewa, tsarin rayuwa sun bambanta daga wuri zuwa wani wurin. Sai an lura dayadda al`adar wuri take da irin tunanin mutanen da ke wurin kafin a sami sahihancin adabin da aka tattara. Ya kamata a lura da yanayin ko walwalar wanda ake hira da shi domin tattara adabin baka, idan an same shi cikin farin ciki, ko shakka babu ana iya samun abubuwan da ake bukata. Idan kuwa yana cikin halin damuwa ko baqin ciki, da wuya a sami biyan bukata, ko an samu ma, bayanan ba su cika kasancewa masu inganci ba.

### 3.3.2 Sauye-Sauyen Al'adu

Kwatankwacin tarihin al`umm, kwatankwacin sauyi na al`adunta, bubuwan da aka samu kafin zuwan baqin al`umma wato cikin al`ummar Hausawa ba za su zamam dai dai da waxanda aka samu bayan cuxanya da baqi ba. Wannan magana haka take, Bahaushe ya yi cuxanya da al`ummomi da dama, adabinsa na kafin addini musulunci daban yake. Bayan ya karvi addini ma adabin sa sun sauya, haka kuma cuxanya da turawa ta samar da adabi daban. Bayan samun `yancin kai kuma adabin ya sauya, Kusan babu wani haqiqanin lokaci na wata al`umma da za a ce gashi a wannan lokaci ne aka fara adabin baka. Don haka, ya kamata mai tattara adabin baka ya san tsarin al`adun al`ummar da yake tattara adabinta,da ire-iren sauye-sauyen da aka samu, idan yana wannan ilimi zai sami abubuwan da yake fata ya samu a wurin waxanda ake nema.

**Auna Fahimta**

1. Me ake nufi da al`ada?
2. Me ya kamata a yi wa mutumin da ake yin hira da shi don tattaro adabin baka?
3. Waxanne sauye-sauye ne adabin baka ya samu lokacin da Bahaushe ya yi hulxa ko dai Larabawa ko kuma Turawa?

## 3.4 Taqaitawa

A wannan darasi, an ga ma`anar al`ada kamar yadda masana suka gabatar, haka kuma, an nuna muhimmancin sanin yadda al`adar mutane take yayin tattara adabin baka, idan ana maganar adabin baka na Bahaushe, yana da kyau a san ire-iren cuxanyar da Hausawa suka yi da baqin al`adu na Larabawa da Turawa waxanda ka iya shafar adabin bakansu. Misali a sanadiyayr musulunci muka sami yin azumi a watan ramalan, wannan azumin ne kuma ya samar da wani nau`in adabin baka mai suna tashe wanda ake yi a yayin da azumi ya kai goma ga wata.

## 3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Al'ada: Hanayar rayuwar al'umma.
- Larabawa: Mutumin da harshensa na haihuwa Larabci ne.
- Azumi: Kame bakai daga barin cid a sha musamman a watan Ramadan.
- Tashe: Wasannin ban dariya da yara suke yi musamman a cikin watan Ramadan.

## 3.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Bunza, A. M. (2002) "Nazarin Al'adun Da Ke Cikin Kaset-Kaset Na Hausa Da Littafan Zamani (1980 – 2002)". Maqalar Da Aka Gabatar A Taron Qarawa Juna Sani Jami'ar Usman Xanfodiyo Sakkwato.

………………. (2006) *Gadon Fexe Al’ada.* Tiwal Nigeria Limited, 16th Akinbaruwa Street, Off Atunrase Street, Surulere, Lagos.

……………….. (2011) “Al’adun Hausawa Jiya da Yau: Ci Gaba ko Lalacewa?” Takardar da Aka Gabatar a Taron Bukukuwan Xalibai na Makon Hausa. Sashen Nazarin Harsuna Nijeriya da Ilimin Harshe, Jami’ar Jihar Kaduna, Kaduna.

Khalil, I. (2009) Cakuxe cakuxen al’adu a fina-finan Hausa. Kundin Digirin Na Biyu Jami’ar Usman Xanfodiyo Sakkwato.

Liman, A. A. (2008) “Hegemony and Mass Mediated Culture: A Study of Popular Culture Trends in Postcolonial Northern Nigeria” Ph.D Thesis. Department of English, Faculty of Arts, Ahmadu Bello University Zaria.

Taylor, E. (1871). *The Science of Culture*. Cambridge University Press.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Amsa Fahimta

1. Me ake nufi da al`ada?

Al’ada tana nufin dukkanin rayuwar ]an Adam tun daga haihuwarsa zuwa kabarinsa’. Wato a ko’ina mutum ya samu kansa, duk wata ]abi’a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu, ko yake rayuwa, ita ce al’adar da za ayi musu hukunci da ita. Saboda haka, babu wata al’umma da za ta rayu a doron }asa face tana da al’dar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata al’ummar daban.

2. Me ya kamata a yi wa mutumin da ake yin hira da shi don tattaro adabin baka?

Ya kamata a lura da yanayin ko walwalar wanda ake hira da shi domin tattara adabin baka, idan an same shi cikin farin ciki, ko shakka babu ana iya samun abubuwan da ake bukata. Idan kuwa yana cikin halin damuwa ko baqin ciki, da wuya a sami biyan bukata, ko an samu ma, bayanan ba su cika kasancewa masu inganci ba.

3. Waxanne sauye-sauye ne adabin baka ya samu lokacin da Bahaushe ya yi hulxa ko dai Larabawa ko kuma Turawa?

Bahaushe ya yi cuxanya da al`ummomi da dama, adabinsa na kafin addini musulunci daban yake. Bayan ya karvi addini ma adabin sa sun sauya, haka kuma cuxanya da turawa ta samar da adabi daban. Bayan samun `yancin kai kuma adabin ya sauya, Kusan babu wani haqiqanin lokaci na wata al`umma da za a ce gashi a wannan lokaci ne aka fara adabin baka. Don haka, ya kamata mai tattara adabin baka ya san tsarin al`adun al`ummar da yake tattara adabinta,da ire-iren sauye-sauyen da aka samu, idan yana wannan ilimi zai sami abubuwan da yake fata ya samu a wurin waxanda ake nema.

## Kashi Na 4: Yiwuwar Ragi ko Qari

**Abubuwan da ke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Ma’anar Ragi
4.3.1 Ragin Yanayi
4.3.2 Ragi na Ma’ana
4.4 Ma’anar Qari
4.4.1 Qari na Yanayi
4.4.2 Qari a Ma’ana
Auna Fahimta na 1
4.5 Taqaitawa
4.6 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

Idan ana maganar adabin baka, ana maganar adabin da ake tattara shi daga bakin mutane, wani lokaci ma ba mutun guda ba, saboda haka, akwai yiyuwar samun ragi ko qari a yayin da ake tattara adabin baka saboda tsawon lokacin da wasu adabin suka yi. Wannan matsala a bayyane take domin kuwa yadda wani ya bayar da tashi fahintar na iya bambanta da yadda aka sami bayanan daga wasu.

### 4.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a san yadda ragi ko qari ke kawo tarnaqi ga tattara adabin baka. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai za su fahimci:

- Ma’anar ragi da qari
- Yadda ragi ko qari ke dakushe sahihancin adabin da aka tattara.
- Bayyana yadda ake samun ragi da qari lokacin da ake tattara adabin baka.

### 4.3 Ma’anar Ragi

Yana da muhimmancin mai karatu ya lura da cewa akwai yiyuwar samun ragi na bayani ko ma`ana ko manufa a lokacin da mutum ke tattara adabin baka. Qamusun Bayero na Kano (2006:363) ya bayyana ragi a matsayin xebe kaxan daga cikin wani abu mai yawa. Wato rage yawan wani abu ko sauqaqa nauyin wani abu. Haka nan kuma an bayyana ragi a matsayin xebe wani abu a cikin farashin asali. Wannan na nuni da cewa ragi shi ne xebe wani abu daba yadda aka san shi.

Ta fuskar tattara adabin baka, ko shakka babu za a sami ragi daga wannan wuri zuwa wancan wuri. Idan labarin ya qunshimisali mutane biyar ne, a wasu wuraren za ka sami labarin na maganaakan mutum uku ne ko huxu. Ba wannan siffar kaxai ba, ragin na iya shafar ire-iren saqonnin da adabi yake xauke dasu matuqar dai an sami ragi a tsarin adabin kamar dai yadda za mu gani nan gaba.

### 4.3.1 Ragin Yanayi

Abu ne mai matuqar muhimmanci a iya rarrabewa tsakanin yanayi nay au da kullum da kuma yanayi na siffa. Idan ana maganar yanayi a nan, ba fa ana nufin irin wanda xan Adam yake rayuwa ba ne, na yanayin damina ko rani ko sanyi ko zafi da dai sauransu. Manufa a nan ita ce, a fahinci cewa yanayi a nan na nufin halin da abu yake ciki, idan mun danganta da adabin baka don gwada yadda ragin yanayi ke zama a matsayin wata matsala ta musamman, to ana nufin rage yadda siffar adabin baka yake. Idan an xauki waqar baka ko zube nab aka ko ma zantukan hikima, za a fahimci abin da ake Magana akai. Bari mu xauki tatsuniya a matsayin misali, idan muka xauki tastuniyar `yar Bora da `yar Mowa, inda aka nuna dukansu sun fita bixar neman Ruwan Bagaja, a wannan tatsuniyar akwai kuguna na abinci da yawa da aka lissafa waxanda sai an qetara su kafin a sami kaiwa ga samun Ruwan Bagaja. Wannan a adabin baka kenan, da aka baddala wannan labari zuwa Qagagge, wanda ya samar da littafin Ruwan Bagaja, an sami sauyi na yanayi, inda maimakon a ambaci nau`o`in abinci da akan ci karo da su yayin bixar, sai kawai a littafin aka musanya da haxarurruka da aka rinqa fuskanta wajen bixar Ruwan Bagaja. Wannan shi ke nuna mana cewa an sami ragi a ainihin yadda adabin bakan yake.

### 4.3.2 Ragi na Ma’ana

A yayin da aka sami sauyin saqo ko manufa ko juya dalilan da suka haifar da wani adabi, to kuwa an sami sauyi na ma`ana. Dukkan ayyukan adabin baka da fasihai suka samar suna da manufar da suke qoqarin isarwa ga jama`a, idan aka sauya masa wannan manufar a lokacin da ake tattara aikin nasa kuwa, an sami sauyi na ma`ana. Yana da kyau a fahinci cewa akwai manufar qirqirar kowane nau`in adabin baka. Yayin wanzar da su waxannan nau`o`in adabin aka sami sauyi na na manufar da ake son cimmawa. Wannan na faruwa ne ga masu wanzar da adabin bakan. Mai tattara adabin baka na iya fuskantar wannan matsala ta ragin manufa. Saboda yakan tunkari mutane da yawa wajen tattara nau`in adabin bakan da yake son tattarawa. Mutanen da yake tuntuva wajen tattara adabin , na iya sauya manufa ko saqon da ake son cimmawa. Wannan na faruwa ta hanyar sauya wasu kalmomi ko tsarin da aka san adabin das hi. Ko ma dai mene ne, shekaru da fahimtar al`amari na iya shafar wanzar da adabin baka daga wannan al`uumma zuwa ga waccan al`umma mai tasowa.

## 4.4 Ma’anar Qari

Za a iya samun qari wajen tattara bayanan da suka shafi adabin baka , ba don komai ba sai kasancewar adabi ne da ake adana shi ta hanyar wanzar

da shi ga al`umma masu tasowa zuwa ga qanana. Idan kuwa abin haka yake, za a iya samun ragi ko qari. Qamusun Bayero, (2006:277) ya bayyana ma`anar qari a matsayin daxin wanin a kan wani abu. Wato daxa wani abu komin qanqanatarsa a bisa siffa ko yanayi na asali da aka san abu da shi, wannan shi ake nufi da qari, wato duk wani abu da ya kasance an sami daxi a kan yadda yake tun asali, an sami qari kenan. Yayin da ake tatattara adabin baka dole a yi la`akari da cewa za a iya samun qari, yana da kyau a tuntuvi mutane da yawa a lokacin da ake tattara wani nau`i na adabi. Idan an tattara daga mutane da yawa sai a zavi bayanan da bakunansu suka zo xaya.

### 4.4.1 Qari na Yanayi

Wannan ma kamar yadda aka yi bayanin ragi na yanayi, haka ma qari na yanayi yake. Shi qarin yanayi xaya vangare ne na ragi, qarin yanayi na nufi duk wani daxi da aka samu na yanayin da abu yake wanda ya sava da asalinsa. Qari ma na xaya daga cikin matsalolin da ke tattare da tattara adabin baka da adana shi. Sauda yawa akan sami sauye-sauyen na yadda adabin baka yake,

### 4.4.2 Qari a Ma'ana

Ma`ana na iya canzawa daga yadda take a lokacin da mutum ya fita tattara adabin baka. Qarin ma`ana na nufin faxar wani abu bisa manufar farko ko fassara ta daban ko nuna wata manufa wadda take qari ne ga ainihin saqon asali.Da yake mutane suke wanzar da adabin baka, kuma halayya da xabi`u da yanayin gudanar da rayuwa sun bambanta, daga wuri zuwa wani wurin, samun qari wajen wanzar da adabin baka abu ne mai sauqi. Wajen taho da adabin baka, ana samun sauye-sauye na qari saboda wasu abubuwa an yi su tun shekaru dubu ko xarurruwa da suka wuce, dole su canza a sami qari wajen wanzar da su daga wannan a[`umma zuwa ga waccan al`ummar.

**Auna Fahimta**

| |
|---|
| 1. Me aka fahimta da sauyi na ma'ana? |
| 2. Shin Ragi ko Qari na iya shafar ingancin tattara adabin baka? |
| 3. Bayyana yadda qarin ma`ana da na yanayi suka kasance matsalolin tattarawa da adana adabin baka. |



## 4.5 Taqaitawa

A taqaice wannan kashi ya nuna ma mai karatu cewa da yawa daga ayyukan adabin baka sun daxe da samuwa tun shekaru aru-aru. Yayin wanzar da su akan sami qari ko ragi na yanayin gudanar da wannan adabi ko ma`anar da wannan adabi yake xauke da su. Ba don komi bas ai don kasancewar adabin ya ratsa zanguna da yawa kuma mutane da yawa sun gudanar da waxannan ayyukan adabin. Misali idan zantukan hikima ne kamar karin magana ko kirari ko take, sukan sami sauyi daga yadda suke na asali.

## 4.6 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Ragi: Yin sauqi a kan yadda wani abu yake.
- Qari: Daxin wani abu a kan wani.
- Ma’ana: Yin bayani a kan wani abu.
- Kirari: Zavavvun kslmomi da ake furtawa a tsare don yin zuga ko kambamawa.

## 4.7 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Bergery, G. P. (1993).*A Hausa –English Dictionary and English Hausa Vocabulary*: Zaria. Ahmadu Bello University Press.

CNHN, (2006): *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers.

## 4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Xaya daga cikin matsalolin tattara adabin baka shi ne Qari, ko an yarda?

Za a iya samun qari wajen tattara bayanan da suka shafi adabin baka , ba don komai ba sai kasancewar adabi ne da ake adana shi ta hanyar wanzar da shi ga al`umma masu tasowa zuwa ga qanana. Idan kuwa abin haka yake, za a iya samun ragi ko qari.

2. Me aka fahimta da sauyi na ma’ana?

A yayin da aka sami sauyin saqo ko manufa ko juya dalilan da suka haifar da wani adabi, to kuwa an sami sauyi na ma`ana. Dukkan ayyukan adabin baka da fasihai suka samar suna da manufar da suke qoqarin isarwa ga jama`a, idan aka sauya masa wannan manufar a lokacin da ake tattara aikin nasa kuwa, an sami sauyi na ma`ana.

3. Bayyana yadda qarin ma`ana da na yanayi suka kasance matsalolin tattarawa da adana adabin baka.

Da yake mutane suke wanzar da adabin baka, kuma halayya da xabi`u da yanayin gudanar da rayuwa sun bambanta, daga wuri zuwa wani wurin, samun qari wajen wanzar da adabin baka abu ne mai sauqi. Wajen taho da adabin baka, ana samun sauye-sauye na qari saboda wasu abubuwa an yi su tun shekaru dubu ko xarurruwa da suka wuce, dole su canza a sami qari wajen wanzar da su daga wannan a[`umma zuwa ga waccan al`ummar.

# RUKUNI NA 4: ZANTUKAN HIKIMAR BAKA NA HAUSA

## Kashi Na 1: Karin Magana

### Abubuwan da ke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Ma'anar Karin Magana ta Zahiri
1.3.1 Ma'anar Karin Magana ta Voye
1.3.2 Zangunan da Karin Magana ya Ratsa
1.3.3 Karin Maganar Dauri
1.3.4 Matsayin Karin Magana a lokacin hulxa da Larabawa
1.3.5 Matsayin Karin Magana a lokacin hulxa da Turawa
Auna Fahimta na 1
1.4 Taqaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Bayanan da ke tattare da karin magana, bayanai masu sauqin fahimta waxanda suka da dangantaka da tarihi. Idan mun duba can da mai nisa, duk zantukan da ake yi na baka ana adana su a 'ka' ne. Amma yanzu ya ratsa wasu zanguna masu yawa waxanda wannan kashi zai duba.



### 1.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce bayyana ma`ana da yadda karin magana ke sauya wa domin su dace da zamanin da ake ciki.



### 1.3 Ma'anar Karin Magana ta Zahiri

Masana da manazarta sun yi ta duduma wajen qoqarin bayyana ma`anar karin magana. Wasu kuwa ba ma`anar kaxai ba, har da irin muhimmancin da ke tattare da Karin magan wajen bayyana falsafar al`umma game da rayuwa. Kirk-Greene (1966) ya bayyana cewa karin magana na inganta al'adun al'umma da suka gada, da tarihin al'umma, da hikimomin al'umma. Bayan haka, a inda ba a sami rubutaccen adabi ba, karin magana na iya zama kafar tattara falsafar qasa. Shi kuwa Zarruq da Alhassan (1982:3) sun bayar da ma'anar karin magana da cewa nazari ne na rayuwa a dunqule cikin gajerun maganganu da misalai irin na hikima. Karin magana ba ta faye zuga ko kuxa ba, sai dai gwanintar kwatance. Misali, "Komai nisan jifa, qasa za ta dawo".

A yayin da waxancan masana suka yi bayanin yadda suke gani sune ma`anonin karin magana, Umar (1984) ya ce, "Karin magana wata

magana ce ‘yar qil da ta qunshi zunzurutun ma’ana lokacin da aka yi bayani. Haka nan Birniwa (2005:57) ya qara bayyana ma’anar karin magana da cewa: “Gajeruwar jimla ce da ake sakaya ma’ana da ita, wadda idan aka warware ta za ta bayar da ma’ana mai tsawo, wadda mafi yawa kalmomin da ke cikinta ba su qunsa ba, sai dai suna da dangantaka da ita”. Duk waxannan ma`anoni da ,masana suka gabatar bas u kawar da bayanan da ke nuna cewa a halin da muke ciki Karin magan ya shi ga wani matsayi na musamman. Da farko dai a ka ake adana shi, daga baya ya ratsa kogin rubutacce inda aka  adanashi a rubutun Ajami, bayan nan ma, ya sake ratsa wani kogin na rubutun boko inda yanzu ya dire a yanar gizo. A kowane kogi da ya ratsa akan sami `yan sauye sauye waxanda suke da dagantaka da lokacin da aka samar da karin maganar. Amma fa a lura dole akwai ma`anar da take nufi na sarari idan an nazarci kalmomin da suka gina Karin maganar, wannan shi ake nufi da ma`ana ta zahiri.

### 1.3.1 Ma’anar Karin Magana ta Voye

Ma`ana ta voye kuwa na nufin saqon da ake so a isar a fakaice, karin magana zance ne a dunqule mai faffaxar ma’ana, wato wata gajeriyar magana ce qunshe da voyayyiyar ma’ana ko dogon bayani in aka warware. Da yake kalmomi biyu ne suka gina karin magana, wato ‘*kari*’ da kuma ‘*magana*’. Kari na nufin wani vangare ko rabi ko karyayye ko kuma rababbe. Magana kuma na nufin zance ko furuci ko kalami da mutum kan yi domin a fahimci abin da ke cikin zuciyarsa. Ke nan karin magana zance ne da aka yi wa givi ko aka karya shi ko raba shi ko kuma aka kawo wani vangare aka yi watsi da wani vangaren (Malumfashi, 2018). Yana da kyau xalibi ya gane ba kalmomi na zahiri ake amfani da su ba wajen bayanin abin da karin magana ke nufi ba, illa saqon da take xauke da shi. Bari mu xauki wani misalin karin magana mai cewa “ Wane ya wuce gona da iri” ma`ana ta zahiri na nufin ya xauki iri yana tafiya har ya wuce gona. Amma ma`ana ta voye kuwa tana nufin wane ya wuce qa`idar da ya kamata ya tsaya, ko ya yi abubuwan da ba su kamata ba. Haka nan kuma, yana da kyau a san cewa karin magana na sauyawa tana tafiya da zamani. Ga wani misalin:

A lokacin mulkin shugaban qasa Jonathan ne aka shiga wani mawuyacin halin rayuwa, ana cikin haka sai kuma ga vullar wata annoba ta Ibola ta shigo qasar Nijeriya, nan da nan sai aka sami wani karin magana “ Ba a rabu da Ebele ba an sami Ebola” Wato ba a fita daga wani qangin ba an faxa wani qangi.

### 1.3.2 Zangunan da Karin Magana ya Ratsa

Da yawa daga cikin karin maganar Hausa sun ratsa zanguna masu yawa, akwai Karin maganar da tun farko a ka suke, daga baya sun sauya a lokacin da aka sami hulxa da larabaewa hak nan zamnin Turawa.

### 1.3.3 Karin Maganar Dauri

Akwai Karin maganar da suke xauke da hoton rayuwar al`umma, wato ta hanyar nazartar waxannan arin maganganun za iya gane tsarin zamantakewar al`ummar Hausawa da tsarin shugabancinsu da yanayin tunaninsu, misalin:- ‘Gyarar fuska ta fi gyarar gona’ ko ‘Shanunka sun bi

Shanun Sarki ko Gaba ta kai ni Gobarar Titi, wa]annan karin maganganun suna bayanin wani lokaci mai tsawo wanda al`umma suka kasance cikin tsananin mulkin sarakuna. Ba Sarki ma hatta dogari da masu Unguwanni tsoransu ake yi.

**1.3.4 Matsayin Karin Magana a lokacin hulxa da Larabawa**

Ko shakka babu hulxa da larabawa ta samar ma Bahaushe da yadda zai yi karatu da rubutu cikin harshen larabci, ba anan abin ya tsaya ba, har ma Bahaushe ya iya fitar da nasa nau`in rubutun na Ajami. Don haka idan aka duba da kyau za a fahinci akwai tasirin musulunci a cikin wasu karin maganganun da suka sami a wannan lokaci. Misali, Taya Allah kiwo ya fi Allah na nan.

**1.3.5 Matsayin Karin Magana a Lokacin Hulxa da Turawa**

Wasu kalmomi ko Magana ko kalamai na hikima sun bambanta da kalamai na yau da kullum, zantukan karin magana galibi gajeru ne masu xauke da dunqulallun ma`ana idan an faxaxa su. Ana amfani da karin magana wajen kaifafa tunani da da cusa kyawawan xabi'u cikin al'umma.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana abin da aka fahimta da karin magana.
2. Waxanne irin saqonni Karin maganar dauri suke nunawa ga al'umma?
3. Faxi matsayin karin maganar Hausa a lokacin hulxa da Larabawa.

## 1.4 Taqaitawa

Karin magana ya kasance xaya daga cikin zantukan hikima na Hausa. A wannan kashi an tattauna a kan ma`ana karin magana ta sarari da ta voye, haka nan kuma an gwada irin zanguna da karin magana ya ratsa waxanda suka taimaka wajen samun sababbi.

## 1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Karin Magana: Magana ta musamman wadda sai an yi tsokaci ake ganewa.
- Zango: tazara da ake samu tsakanin garuruwa ko faruwar wani abu.
- Hikima: Yin wani abu day a burge mutane.
- Zance: Taxi tsakanin mutum biyu ko fiye.

## 1.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Birniwa, H.A. (2005). Tsintar Dame a Kala : Matsayin Karin Magana a Cikin Waqoqin Siyasa. In Xunxaye Journal of Hausa Studies.

Department of Nigerian Languages. Sokoto : Usman Xanfodiyo University.

Bunza, A.M (2006). Gadon Fexe Al'ada. Lagos : Tiwal Nigeria Limited.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

Kirk-Greene, A.H.M (1996). Hausa Ba Dabo Ba Ne. Ibadan : Oxford University Press.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Bayyana abin da aka fahimta da karin magana

Karin magana nazari ne na rayuwa a dunqule cikin gajerun maganganu da misalai irin na hikima. Karin magana ba ta faye zuga ko kuxa ba, sai dai gwanintar kwatance. Misali, "Komai nisan jifa, qasa za ta dawo".

2. Waxanne irin saqonni Karin maganar dauri suke nunawa ga al'umma?

Akwai karin maganar da suke xauke da hoton rayuwar al`umma, wato ta hanyar nazartar waxannan arin maganganun za iya gane tsarin zamantakewar al`ummar Hausawa da tsarin shugabancinsu da yanayin tunaninsu, misalin:- 'Gyarar fuska ta fi gyarar gona' ko 'Shanunka sun bi Shanun Sarki ko Gaba ta kai ni Gobarar Titi, wa]annan karin maganganun suna bayanin wani lokaci mai tsawo wanda al`umma suka kasance cikin tsananin mulkin sarakuna. Ba Sarki ma hatta dogari da masu Unguwanni tsoransu ake yi.

3. Faxi matsayin karin maganar Hausa a lokacin hulxa da Larabawa.

Ko shakka babu hulxa da larabawa ta samar ma Bahaushe da yadda zai yi karatu da rubutu cikin harshen larabci, ba anan abin ya tsaya ba, har ma Bahaushe ya iya fitar da nasa nau`in rubutun na Ajami. Don haka idan aka duba da kyau za a fahinci akwai tasirin musulunci a cikin wasu karin maganganun da suka sami a wannan lokaci. Misali, Taya Allah kiwo ya fi Allah na nan.

## Kashi Na 2: Salon Magana

**Abubuwan da ke Ciki**

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Ma’anar Salo
2.3.1 Ma’anar Salon Magana
2.3.2 Salailan Magana
2.3.3 Karin Maganar Dauri
2.3.4 Matsayin Karin Magana a lokacin hulxa da Larabawa
2.3.5 Matsayin Karin Magana a lokacin hulxa da Turawa
Auna Fahimta na 1
2.4 Taqaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 2.1 Gabatarwa

Da jin sunan ma an san akwai gwanintar harshe da qyale-qyalen zance, salo zavi ne na mai magana, wato ba dole ne a yi maganar kara zube ba, saboda haka Salon magana ko qarangiya ko gagara-gwari xaya ce daga cikin hikimomin sarrafa harshe da Bahaushe ke amfani da su a zantukansa na yau da kullum domin qawata zance da qara armashin magana.
Wannan kashi ya qunshi bayanai kan salon magana da ire-irensa a Hausa.



### 2.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da salon magana a adabin Hausa da ire-iren salon maganar. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai za su fahimci ma`anar salo shi kanshi, da ma`anar salon magana har da ire-irenta.



### 2.3 Ma’anar Salo

Masanin adabin Hausa, Xangambo (1981:2-3), ya bayyana ma’anar salo a matsayin hanyoyi ko dabarun isar da saqo. Wato salo ya qunshi zavi kuma kyan salo ko muninsa ya danganta da yadda mutum ya zavi abubuwan da ya yi amafani da su cikin rubutunsa ko furucinsa don isar da saqonsa. Salo ya ta’allaqa ne dangane da yadda mutum yake tunani cikin dacewa.

#### 2.3.1 Ma’anar Salon Magana

Salon magana maganganu ne na hikima da kakkarya harshe waxanda ake yi ta hanyar sarqa kalmomi masu sauti iri xaya a cikin jimla ko jimloli, a

yi magana mai sarqaqiya. Haka nan kuma, salon magana wanda wasu ke kira qarangiya ko gagara-gwari zance ne mai xauke ko qunshe da wasu kalmomi masu wuya ko masu kama da juna, yakan qunshi luguden kalmomi.

### 2.3.2 Salailan Salon Magana

Salon Magana na da yawa a harshen Hausa, gwargwadon naqaltar harshen mai magana. Mislai:

- Tun da Tava take ba ta tava tava tavo ba, ga shi yau Tava ta tavo tavo.
- Turmi ture kura, kura ture turmi.
- Cab cave qashi, tsoka, tsotse, soke a faqo.
- Ina tafiya ta Kurun na tsinci kunkurun Kurun na kai ta kasuwar Kurun ana kurun ina kurun na sai da kunkurun Kurun.
- Haka silif na saluve siliya a wuyan Salamatu ashe ban sani ba an yi wa Salihu satar sintali a Salanta.
- Battar da ba ta da taba ba ta tabbata batta ba da tana da taba da ta tabbata batta.
- An kashe kasa, an kasa gwaza, garin kallon kasasshiyar kasa na kasa kwashe kashin gwaza.

**Auna Fahimta**

1. Salo suna suka tara, amma kowanne da salonsa . Tattauna
2. Bayyana abin da ka fahimta da salon magana.
3. Kawo misalan salon magana guda biyar (5) da ka sani.

## 2.4 Taqaitawa

Muhimman batutuwan da wannan darasi ya duba sun haxa ma`anar salon magana da ire-irensa a matsayin dabarun qawata zance na yau da kullum. Kashin ya qunshi bayanai kan ma’ana da ire-iren salon magana tare da misalai. Faxin kalmomin ko jimlolin cikin sauri shi ke nuna gwanintar mutum.

## 2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Magana: Zance da aka furta a magance ko a rubuce domin isar da wani saqo.
- Salo: Hanya ko dabara da aka bi wajen isar da saqo.
- Qawatawa: Yin abu ya yi kyau sosai don a burge jama’a.
- Jumla: Cikakken zance mai xauke da ma’ana tare da bin wasu qa’idodji

## 2.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Salo suna suka tara, amma kowanne da salonsa. Tattauna

An bayyana ma'anar salo a matsayin hanyoyi ko dabarun isar da saqo. Wato salo ya qunshi zavi kuma kyan salo ko muninsa ya danganta da yadda mutum ya zavi abubuwan da ya yi amafani da su cikin rubutunsa ko furucinsa don isar da saqonsa. Salo ya ta'allaqa ne dangane da yadda mutum yake tunani cikin dacewa.

2. Bayyana abin da ka fahimta da salon magana.

Salon magana maganganu ne na hikima da kakkarya harshe waxanda ake yi ta hanyar sarqa kalmomi masu sauti iri xaya a cikin jimla ko jimloli, a yi magana mai sarqaqiya.

3. Kawo misalan salon magana guda biyar (5) da ka sani.

- Tun da Tava take ba ta tava tava tavo ba, ga shi yau Tava ta tavo tavo.
- Turmi ture kura, kura ture turmi.
- Cab cave qashi, tsoka, tsotse, soke a faqo.
- Ina tafiya ta Kurun na tsinci kunkurun Kurun na kai ta kasuwar Kurun ana kurun ina kurun na sai da kunkurun Kurun.
- Haka silif na saluve siliya a wuyan Salamatu ashe ban sani ba an yi wa Salihu satar sintali a Salanta.

**Kashi Na 3: Take da Kirari**
**Abubuwan da ke Ciki**

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Ma’anar Take
3.3.1 Ma’anar Kirari
3.3.2 Bambancin Take Da Kirari
Auna Fahimta na 1
2.4 Taqaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 3.1 Gabatarwa

Take da kirari tamkar abokan juna ne domin a mafi yawancin lokuta tare suke tafiya ko kuma take ya yi wa kirari sharar fage. Wannan kashi ya qunshi bayani kan ma’anar take da kirari da kuma bambance-bambancen da ke tsakaninsu.



## 3.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da take da kirari a adabin Hausa da ire-irensu da kuma bambancin take da kirari. A qarshen wannan darasin, ana sa rai xalibai za su fahimci :

a- Ma’anar Take
b- Ma’anar Kirari
c- Bambancin Take da Kirari



## 3.3 Ma’anar Take

Shi Take kamar sauran sassan adabin bakan Hausawa abu ne da ya shafi ki]a da wa}a kuma galibi wa}ar baka da ta zo da ki]a to bu]inta shi ne take. Shi ya sa masana ke cewa ‘take wani guntun amo ko zance ne na share fage wata}ila kafin kirari ya iso’. Yana zuwa ne a salon ki]a ko busa ko wanin wa]annan wanda akan fassara cikin magana. Haka kuma take na iya zama wani ~angare na }o}arin yabo ko kushewa ga abubuwan da jama’a suka sa gaba na ra’in kansu shi yake haifar da take da kirari. Akan yi wa maza tuni da wani kakansu jarumi ko wanda ya yi fice kan wata sana’a ta wannan fasali. Muna iya cewa ke nan take wata shimfi]a ce ta amfani da harshe wajen tayar da tsinkar jikin mutum, kuma abin da zai biyo a kan wannan shimfi]ar shi ne kirari, kuma take bai cika tsawo

ba.Saboda haka za a samu cewa take na zuwa ne da fasalin ki]a ko busa ko gogawa ko makamantan haka. Shi da yake ba zance ko furuci ne ba yana zuwa da amo ne, da zarar aka yi wa mutum take tana yiwuwa ya ~uge da yin kirari.

**3.3.1 Ma'anar Kirari**

Kirari kuwa ]aya daga cikin rukunin adabin bakan Bahaushe da ya gada tun kaka da kakanni, don haka ba wata al'umma da za ta yi i}irarin cewa ita ta koya wa Bahaushe hikimar aiwatar da kirari. Masana adabin Hausa sun ba da ma'anar kirari gwargwadon fahimtarsu, dangane da yadda ya shafi al'amurran Hausawa da kuma yadda su suka cu]anya da shi. Bargery ya bayar da ma'anar kirari a }amus ]insa da cewa wa]ansu maganganu ne da ake yi wa sarakuna ko muhimman mutane da suke bayyana halayensu da kuma kamanninsu ta hanyar kambamawa. Wasu masanan na ganin kirari da cewa wani abu ne wanda ya yi kama da yabo, haka kuma a duk lokacin da ]anma'abba yake rera shi za ka ji kamar wa}a, ko kuma wani irin jawabi ne aunanne da ake fa]a da baka, a yayin da masu wasanni, kamar mafarauta ko 'yan dambe ko 'yan kokawa suke yi. Ana iya yi wa kowa kirari idan ya yi fice a sana`arsa ko a cikin jama`a saboda wata baiwa ta musamman. Ana kuma iya yi wa mutum kirari kamar haka:

> Gamji ]an }warai
> Naira yayinki a kai ko'ina…
> Gamzaki mai fita da subahi
> Zaki mai }ashi guda…
> Giwa kin wuce }aho…
> |auna sanuwar sake …

**3.3.2 Bambancin Take da Kirari**

Take, abu ne da ake danganta shi da bayyana wanda ake yabo, wato taken wani ya sha bamban da na wani, misali, irin taken da ake yi wa samari da 'yammata wurin kixan kalangu da sauransu. Kirari kuwa, yana iya zama yabon kai, kamar yadda 'yan tauri ko 'yan dambe ke yi; ko kuma yabon wani, kamar yadda maroqa ke yi, da sauransu. Take wani amo ko zance da ke share fage kafin kirari ya iso. Ana yin take ne da kixa ko busa ko wani salo da za a iya fassarawa a maganance. Misali, kafin fara farauta akan yi kixa don sanar da jama'a cewa za a fita, kuma wannan kixan yakan zo a matsayin taken wani xan farauta ne. Sa'annan take kan iya zama wani vangare na qoqarin yabo ko kushewa ga abubuwan da jama'a suka sa gaba, sai dai take bai cika tsawo ba. Sai dai duk da yake take yana zuwa da amo ne, ba zance ko furuci ne ba, da zarar aka yi wa mutum take zai iya vugewa da yin kirari.

A tsarin kirari, za a kira mutum ne ta hanyar amfani da sunansa ko ta ambaton siffofinsa waxanda abin tutiya ne ko a wajen mai yin kirarin. Har ila yau, kirari kan iya qunsar kalaman da in ba a muhalli na kirarin ba, ba sa ambatuwa kai-tsaye ga mutum. Misali kalmomi irin su 'shege' ko 'mahaukaci' ko 'arne' da sauransu.

**Auna Fahimta**

1. Kawo ma'anar kirari tare da misalan kirarin da ake wa mutum guda uku (3)
2. Bayyana bambance-bambancen da ke tsakanin take da kirari.
3. Take shi yake share fage kafin kirari ya iso. Ka yarda?

## 3.4 Taqaitawa

Daga bayanan da suka gabata, mun fahimci ma`anar take da kirari da kuma bambance-bambancensu, ana gina kirari da siffa ko halayyar mutum ko abin da za a kirara, akan kuma danganta abu da makusantarsa misali miji da mata ko 'yan'uwa da sauransu. Sa'annan, ana iya yi wa mutum ko dabba ko gari ko abinci ko itaciya ko wani abu mai rai ko mara rai kirari. Shi kuwa take amo ne ake kaxawa domin tsuma mutum (galibi) a fagen nuna bajinta kamar farauta ko yaqi da sauransu). Sai dai kirari kan biyo bayan take ya yi masa ladanci.

## 3.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Take: Nau'in kirarin da makaxa suke yi wa iyayen gidansu ko jarumai ko samari.
- Kirari: Zavavvun kalmomi da ake furtawa a tsare don zuga ko kambamawa.
- Bajinta: Qwazo ko jaruntaka ko nuna qasaita.
- Amo: Murya ko sauti ko qara.

## 3.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari

Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Kawo ma'anar kirari tare da misalan kirarin da ake wa mutum guda uku (3)

kirari da cewa wani abu ne wanda ya yi kama da yabo, haka kuma a duk lokacin da ]an ma'abba yake rera shi za ka ji kamar wa}a, ko kuma wani irin jawabi ne aunanne da ake fa]a da baka, a yayin da masu wasanni, kamar mafarauta ko 'yan dambe ko 'yan kokawa suke yi. Ana iya yi wa kowa kirari idan ya yi fice a sana`arsa ko a cikin jama`a saboda wata baiwa ta musamman. Ana kuma iya yi wa mutum kirari kamar haka:

Gamji ]an }warai
Naira yayinki a kai ko'ina…
Gamzaki mai fita da subahi

2. Bayyana bambance-bambancen da ke tsakanin take da kirari.

Take, abu ne da ake danganta shi da bayyana wanda ake yabo, wato taken wani ya sha bamban da na wani, misali, irin taken da ake yi wa samari da 'yammata wurin kixan kalangu da sauransu. Kirari kuwa, yana iya zama yabon kai, kamar yadda 'yan tauri ko 'yan dambe ke yi; ko kuma yabon wani, kamar yadda maroqa ke yi, da sauransu.

3. Take shi yake share fage kafin kirari ya iso. Ka yarda?

Take wani amo ko zance da ke share fage kafin kirari ya iso. Ana yin take ne da kixa ko busa ko wani salo da za a iya fassarawa a magananance. Misali, kafin fara farauta akan yi kixa don sanar da jama'a cewa za a fita, kuma wannan kixan yakan zo a matsayin taken wani xan farauta ne.

**Kashi Na 4: Zaurance**

**Abubuwan da ke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Ma’anar Zaurance
4.3.1 Ire-Iren Zaurance
4.3.2 Yadda Ake Aiwatar da Zaurance
Auna Fahimta na 1
4.4 Taqaitawa
4.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Qarin Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

Wani salon na nuna gwanintar harshe shi ne Zaurance, Bahaushe na amfani da shi do nuna qwarewa da bajinta kakkarya harshe. Galibi an fi sanin matan Hausawa da zaurance. A taqaice zaurance wani salo ne na qwarewar harshe da Hausawa ke amfani da shi a matsayin sadarwa ta sirri a tsakanin su.

## 4.2 Manufofin Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da abin da ake nufi da zaurance, in har an fahimta xalibi ya iya qirqirar tasa zaurancen.

## 4.3 Ma’anar Zaurance

Shi ma Zaurance tamkar salon magana ne da akan yi don a ɓad-da bami, domin kada ya gane inda aka dosa. Zaurance kan kasance tamkar wani yare ne na ɗan taƙaitaccen lokaci da ake ƙirƙira a cikin rukunin al’umma, saboda a nuna gwanancewa a harshe.

Masana irin su Xangambo, (2008) sun bayyana Zaurance da cewa: shi ma sarrafa harshe ne, da ke cike da hikima. Zaurance, qirqirarren harshe ne. Akan qara wa kalmomi ko kuma gavovin kalmomi wasu kalmomin ko gavovin, a mai da su sababbi, yadda idan mutum bai naqalci yadda abin yake ba, to, ba zai gane abin da ake nufi ba. Ana iya qara duk abin da aka ga dama, don a yi wannan vad-da-bami. Misali, za a iya qara wa gavovin kalmomi sautukan b,c,d,f,g,h,j,k, da dai sauransu. Ga wani misalin zaurance wanda ake qara *da:*

Musa = Mu-du-sa-da = Mudusada
Mairo= Ma-dai-ro-do = Madairodo
Ka-dai ma-dai ka-da-ra-da-tu-du = kai mai karatu

Za-dan-ce-de, ko-do ba-da ka-da = zan ce ko ba ka gane ba? ga-da-ne-de- ba-da?

Na-da-je-de-ka-da-su-du-wa-da = Na je kasuwa.

**Shin k**ai mai karatu, ka gane wannan zance, ko ba ka gane ba? A nan, za a lura cewa, ana qara wa gavovin kalmomi da ne, sai dai qarin, yana shafar wasulla ma; idan ma akwai xauri, baqi (harafi), shi ma abin yana shafar sa.

Misali:

Idan gavar tana da wasalin *a*, to *d* xin da aka qara, shi ma sai a sa masa *a*, idan *e* ne, sai a sa wa *d* xin e, da dai sauransu. Idan kuwa xauri ne, misali, *kai, sai, mai, tau, qin* da sauransu, to, nan ma, akan yi wa haruffan xaurin bayan *d* xin. Misali, *ka-dai, sa- dai, ma-dai, ta-dau, qi-din,* da sauransu.

### 4.3.1 Ire-Iren Zaurance

Abin da ke sama misali ne na zaurance guda xaya. Za a iya samun zaurance iri daban daban, wannan ya danganta da irin qarin da aka yi wa kalma ko kuma gavovin muryoyin kalmonmi.

### 4.3.2 Yadda Ake Aiwatar da Zaurance

Kamar yadda aka bayyana a baya, ana samun zaurance ne ta hanyar ƙara wasu harrufa a ƙarshen kowace gaɓa da ke cikin kalma har zuwa ƙarshen zancen,har ila yau, babu wata ƙa'ida da aka ajiye cewa lallai sai harafi kaza za a yi amfani da shi. Idan ma akwai zavi na musamman masu yin zaurancen ne sukan zaɓi salon da suka so. Shi ya sa ma waɗannan ba su gane na waɗancan.

**Auna Fahimta**

1. Me ka fahinta da zaurance ?
2. Kawo misalan zaurance guda uku (3) wanda ake qara ***da***
3. Ta yaya ake harhaxa kalmomin zaurance?

## 4.4 Taqaitawa

Bayanai sun gabata masu nuna cewa 'Yan mata ne suka fi yin zaurance, musamman a lokacin da suke son yin wata magana ta sirri a tsakaninsu wadda ba su son kowa ya fahimta sai su kaɗai, sukan tsaya su tsara salon da za su riƙa yin maganar da ba mai iya gane ta sai su kaɗai. Zaurance salo ne na qwarewar harshe da Hausawa ke amfani da shi a matsayin sadarwa ta sirri a tsakanin su. Baya ga gwanintar harshe, zaurance na koyar da muhimmancin riƙe sirri da neman shawarar juna da haɗin kai da amince wa juna da riƙon amana, da kuma son juna.

## 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Zaurance: Salon magana da ake yi don nuna qwarewar harshe wajen isar da saqo
- Sirri: Abin da ba a so a ji, ko gani, ko kuma a sani.
- Amana: Ajiya ko adana wani abu kamar yadda aka bayar da shi.
- Qwarewa: Iya aikata wani sosai.

**4.6 Manazarta da Waxansu Abubuwa na Qara Nazari**


Xangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

Abrams, M.H. (1981): *A Glossary of Literary Terms.* Six Edition Halt Rinehart & Wiston, New York.

Abdullahi, B.Y. (2001): *Salo Asirin Waka* Fisbas Media Kaduna.

Ahmed, U.B (1985) *Nau'o'in wasannin kwaikwayon Hausa.* Cibiyar Nazarin Al'adun Nijeriya. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Ayindaho, K. (1985) "The Present State of African Literature Studies" In *African Literature Studies: The Present State*. Ed Stephen Arnold, Washington; African Literature Association & Three Continent's Press.

Babajo, A. K. (2011). *Orature: Meaning, Nature and Forms*. A Study Guide for Undergraduate, Kaduna: Slimline Communication.

Bergery, G. P. (1993).*A Hausa –English Dictionary and English Hausa Vocabulary*: Zaria. Ahmadu Bello University Press.

Birniwa, H.A. (2005). Tsintar Dame a Kala : Matsayin Karin Magana a Cikin Waqoqin Siyasa. In Xunxaye Journal of Hausa Studies. Department of Nigerian Languages. Sokoto : Usman Xanfodiyo University.

Bunza, A. M. (2002) "Nazarin Al'adun Da Ke Cikin Kaset-Kaset Na Hausa Da Littafan Zamani (1980 – 2002)". Maqalar Da Aka Gabatar A Taron Qarawa Juna Sani Jami'ar Usman Xanfodiyo Sakkwato.

………………. (2006) *Gadon Fexe Al'ada.* Tiwal Nigeria Limited, 16th Akinbaruwa Street, Off Atunrase Street, Surulere, Lagos.

……………….. (2011) "Al'adun Hausawa Jiya da Yau: Ci Gaba ko Lalacewa?" Takardar da Aka Gabatar a Taron Bukukuwan Xalibai na Makon Hausa. Sashen Nazarin Harsuna Nijeriya da Ilimin Harshe, Jami'ar Jihar Kaduna, Kaduna.

Cuddons, J.A (1977).*A Dictionary of Literary Terms*.Revised Edition, London.

Xangambo, A. (1984): *Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph Publishers.

Xangambo, A. (2007). *Xaurayar Gadon Fexe Waqa*. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Finnegan, R. (1970). *Oral Literature in Africa*. Oxford: Oxford University Press.

Garba, S. (2011). "Salon Sarrafa Harshe A Waqoqin Aqilu Aliyu". Kundin Digiri na Uku. Zariya: Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Services.

………………(2003). *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka*. Benchmark Publishers Limited, Kano.

………………(2006). Tatsuniya (Gatana) : Sigoginta da Hikimominta. Cikin *Mujallar Algaita*, 4,1.

………………(2008). *Waqoqin Baka A Qasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu*. Kano: Benchmark Pulishers Limited.

………………(2009). Diwanin Waqoqin Baka: Zavavvun Matanoni Na Waqoqin Baka Na Hausa. Kano: Century Research and Publishing Limited.

………………(2014) *Diwanin Waqoqin Baka*. Juzu'i Na Biyu: Century Research and Publishing Limited Kano-Nigeria.

Khalil, I. (2009) Cakuxe cakuxen al'adu a fina-finan Hausa. Kundin Digirin Na Biyu Jami'ar Usman Xanfodiyo Sakkwato.

Kirk-Greene, A.H.M (1996). Hausa Ba Dabo Ba Ne. Ibadan : Oxford University Press.

Lado, R. (1964): *Language Teaching* – A Scientific Approach, McGraw-Hill: New York.

Lenneberg, E. H. (1967): *Biological Foundations of Language*, Wiley, New York.

Liman, A. A. (2008) "Hegemony and Mass Mediated Culture: A Study of Popular Culture Trends in Postcolonial Northern Nigeria" Ph.D Thesis. Department of English, Faculty of Arts, Ahmadu Bello University Zaria.

Lorentzon, L. (2007). Is African Oral Literature Literature? *Research in African Literatures,38*(3), 1-12. Retrieved February 7, 2020, from www.jstor.org/stable/20109492

Malumfashi, I. (2019): "Kunnenka Nawa? Labarin Hausa a Rubuce" a Cikin *Labarin Hausa a Rubuce1927-2018* ISSBN: 978:978-55352-8-0. Zariya: Xab'in Maxaba'ar Jami'ar Ahmadu Bello

Muhammad, X.(1978). "Waqa Bahaushiya". cikin *Studies in Hausa Language, Literature And Culture*. Kano: Bayero University.

Mujaheed, A. (2018). "Hankaka Mai Da Xan Wani Naka: Waqoqin Salisu Sa'inMakafin Zazzau a Bakin Mawaqan Qarni na 21". *Kadaura: Journal of Hausa Multi-Disciplinary Studies*, Vol. 1, No. 4, Special Edition. Department of Nigerian Languages and Linguistics, Kaduna State University-Nigeria.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin {agaggun Labarai*. Benchmark Publishers Limited, Kano.

……………..(2004). *Introduction To Stylistics Theories, Practice And Criticism*. Abuja; Country Side Publishers Vol. I.

Okoh, Nkem. (2008). *Preface to Oral Literature*, Africana First Publishers Limited, Books House Trust, Onitsha Nigeria.

Okpewho, I. (1990). *Oral Performance in Africa*. Ibadan Spectrum Books. Ltd.

…………. (1992). *African Oral Literature*. Bloomington IN Indiana University Press.

Rabi, M. (2011): "Xabi'un Mata a Bakin Mawaqan Baka na Hausa" Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsuna da Al'adun Afrika, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya (2013) *Makaxi A Mahangar Manazarta:* Jerin Takardun da Aka Gabatar a Taron Qara wa Juna Sani Kan Tubar Muhammadu Gambo Mai Kalangu, Gidan Dabino Publishers.

Satatima, I.G.(2009). "Waqoqin Baka na Xarsashin Zuciya: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu." Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Shipley, J.T. (ed) (1955).*Dictionaryof World Literary Terms.*Allens & Unwin Ltd London.

Taylor, E. (1871). *The Science of Culture*. Cambridge University Press.

Yakasai, S A. (2012). *Jagorar ilimin Walwalar Harshe*, Sokoto. Garkuwa Media Service Ltd.

Yahaya, A. B. (1997). *Jigon Nazarin Wa}a* Fisbas Media Service Kaduna.

Yahaya, I.Y. (da wasu) (1992).*Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare*1 – 3, Ibadan University Press.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ka fahinta da zaurance?

Shi ma Zaurance tamkar salon magana ne da akan yi don a ɓad-da bami, domin kada ya gane inda aka dosa. Zaurance kan kasance tamkar wani yare ne na ɗan taƙaitaccen lokaci da ake ƙirƙira a cikin rukunin al’umma, saboda a nuna gwanancewa a harshe.

2. Kawo misalan zaurance guda uku (3) wanda ake qara ***da***

| | | |
|---|---|---|
| Musa | = Mu-du-sa-da | = Mudusada |
| Mairo | = Ma-dai-ro-do | = Madairodo |

Ka-dai ma-dai ka-da-ra-da-tu-du = kai mai karatu

3. Ta yaya ake harhaxa kalmomin zaurance?

Ana samun zaurance ne ta hanyar ƙara wasu harrufa a ƙarshen kowace gaɓa da ke cikin kalma har zuwa ƙarshen zancen,har ila yau, babu wata ƙa’ida da aka ajiye cewa lallai sai harafi kaza za a yi amfani da shi. Idan ma akwai zavi na musamman masu yin zaurancen ne sukan zaɓi salon da suka so. Shi ya sa ma waɗannan ba su gane na waɗancan.